# ƘASAR ZAMFARA A BAKIN ALHAJI MUSA ***ƊANƘWAIRO*** MARADUN

Daga

Alhaji Ibrahim Muhammad
*Ɗanmadamin Birnin Magaji*
Fadar Mai Martaba Sarkin Birnin-Magaji (Ɗan Alin Birnin-Magaji),
Jihar Zamfara. 08149388452, birninbagaji4040@gmail.com

Takardar da Aka Gabatar a Taron Ƙasa da Ƙasa Kan Tarihin Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun da Waƙoƙinsa, A Cibiyar Nazarin Harsuna Al'adu da Fassara, ta Jami'ar Bayero, Kano Ranar 13 Satumba. 2021

ƘASAR ZAMFARA A BAKIN ALHAJI MUSA ***ƊANƘWAIRO*** MARADUN

**Tsakure**

Wannan aiki a kan Makaɗa Musa Ɗanƙwairo ne. Za a dubi fasihancinsa na adana tarihin ƙasar Zamfara a waƙe. Idan aka dubi ayyukan da suka gabaci wannan maƙala kan Alhaji Musa Ɗanƙwairo, za a daidaita sahun tunanin duk abinda aka ci karo da shi ta hanyar binciken Tarihinsa da tarihin waƙoƙinsa a bakin 'ya'ya da jikoki da aminansa waɗanda ke raye. Wannan zai kai wannan bincike ga amfani da nau'in bincike na tattaunawa da kai ziyarar gani da ido a wurin mutane da wurare daban-daban. Wannan zai samu jagorancin ra'o'i guda biyu: Ra'in Tushe da Asali da Ra'in Fandarewa. Wadannan ra'o'i sun tsayu a cikin wannan aiki domin sanin asalin Musa Dankwairo, da kuma taskace tarihinsa da wakokinsa a cikin ayyukan da aka gabatar kansa. A fahimtar da na yi wa Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun saboda sauraren waƙoƙinsa da nake yi tsawon lokaci, yana da matsayin da tarihin mawaƙan ƙasar Hausa da na Zamfara ba zai cika ba, ba tare da kawo sunansa da waƙoƙinsa ba. Fasihancinsa a waƙe, ya zama tamkar kotun yanke hukunci ga kowane al'amari na rayuwa.

## 1.0 Gabatarwa

Idan ana neman tarihi na mutum (al'ummu), ko ƙasa ko dabba, ko wani al'amari, to ana komawa ga adabin baka na waɗannan mutanen domin ganin yadda hoton abinda ake magana a kai yake, ko ya kasance. Abubuwan da za a nema na adabin baka bai wuce Tarihi na baka, da tatsuniyoyimmu, da karorin maganganummu da sauran maganganun azancimmu ba. Wata taska ta adabi da ake yawan leƙawa domin neman tarihi ita ce waƙa ta baka (har ma da rubutacciya[1]) irin wannan leƙe na neman tarihi za a yi wa tarihin Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun. A tsarin wannan maƙala an so a nemo wasu kundaye ko wallafe-wallafe ko tsokaci na baka waɗanda aka gabatar a kan rayuwa da fasihanci Makaɗa Musa Ɗanƙwairo domin taskace tarihinsa wanda ke da ruwayoyi daban-daban a hannun manazarta. Haka nan za a yi nazarin wasu daga cikin waƙoƙin Ɗanƙwairo domin a ga yadda ya naɗe tarihin ƙasar Zamfara a cikin taushensa. Matashiyarmu mun ambata cewa idan za a leƙa tarihin wani abu kamar al'umma ko ƙasa ana leƙa adabin baka, to a wannan tsarin za a yi nazarin tarihin Zamfara ta fuskokin ƙarhin Mulki, Kasuwanci da yanayin ƙasa da al'ummar wannan yanki. Za a yi ƙoƙarin dogara kowane Ambato da tushen bayani ko Tubalai domin neman ƙarin haske.

### 1.1 Ra'in Tushe da Asali da Ra'in Fanɗarewa

Ayyukan da aka yi bita waɗanda za a gansu a tushen bayanin kowane shafi da kuma shafin manazarta sun ƙara ba da haske ga zaɓar ra'in da aka tunƙa zaren wannnan maƙalar da shi. A ƙoƙarin fahimtar Ra'in da bayaninsa, an ɗauko ma'anar Ra'i bisa fahimtar malaman da ke yin tarke ga ayyukan adabi ko na Al'adun mutane.

#### 1.1.1 Ma'anar Ra'i

Ra'i tunani ne, ko jerin tunane-tunane da aka shawarta cewa su ne ke iya bayanin abinda ya faru, ko kuma wanda zai faru (ƙamusun Oxford, 1998:480)

---

[1] . Ana adana tarihi a cikin rubutacciyar waƙa bayan Hausawa sun samu fasahar karatu da rubutu. Tarihimmu yana adane cikin waƙoƙin da ke cikin ajami da Hausar Boko, amma kafin samuwar rubutu ga Hausawa, waƙar baka ita ce taskar adana kowane irin tarihi na al'ummar Hausawa.

Ra'i wani silalen zaren tunani ne kan wasu batutuwa waɗanda ke zama a matsayin wani mizani wanda za a iya yin amfani da shi domin auna irin abubuwan da ke aukuwa a duniya, domin a tsara abin ta yadda za a fahimce shi (Kenan, 2008:01)

Ra'i hasashe ne, wanda in an kalle shi da kyau za a ga gaskiyar abin, amma kuma yana iya kasancewa ba Gaskiya ba (Longman, 2003: 692)

### 1.1.2 Dangantakar Ra'i da Saƙon Wannan Maƙala

Waɗannan ra'o'i guda biyu sun fassara tunanin wannan maƙala, inda ra'in farko na neman asali zai jagoranci nema da bayyana asalin tarihin mutane musamman waɗanda suka shuɗe, domin adana tarihinsu na gaskiya kada ya salwanta / salwance saboda tawilin yau da gobe. ***Daga cikin abinda aka yi nazari na Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun an fahimci ruwayoyin manazarta suna cin karo da juna kan shekarun***

***Musa Ɗanƙwairo da wasu bayanai da suka danganci rayuwarsa. Ra'i na biyu zai jagoranci wani bayani na fanɗarewa inda za a kalli dalilan da suka haifar da samun ruwayoyi***

***kan rayuwar Makaɗa Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun***

Bisa jagorancin waɗannan ra'o'i aka bibiyi tarihin Ɗanƙwairo musamman ta nasabar iyaye da kakanni, da kuma a fasihance inda aka ji daga bakin shi kansa Ɗanƙwairon matsayin da ya yi ma kansa ta fuskar waƙa, da kuma yadda wasu mawaƙa ke kallonsa a farfajiyar waƙar baka dk a babin da zai biyo wannan.

Haka nan ra'in fanɗarewa ya samu walwala a cikin wannan maƙala saboda abubuwa guda biyu:

Na farko shi ne, Alhaji Musa Usman Ɗanƙwairo Maradun ya bayyana a cikin tarihin kansa da aka tattauana da shi[2] cewa yana tsammanin shekarunsa 60 (sittin)[3] wanda idan aka auna wannan magana tashi da waɗanda suka yi zamani da shi a wannan lokaci ya yi daidai da cewa Ɗanƙwairo ya zarta waɗannan shekarun da kimamnin shekaru shabiyu (12), domin hujjar da

---

[2] . An yi Hira da Ɗanƙwairo a ranar 8 /11/1974 a gidan Rediyo Nijeriya na Kaduna acikin shirin "Makaɗa da mawaƙa" wanda shiri ne da aka fito da shi domin tattaunawa da fitaccin mawaƙan baka a faɗin arewacin Nijeriya.

[3] . A lokacin da aka ayi wannan tattaunawa da Alhaji Musa Ɗanƙwairo a shekarar 1974 ne, wanda lokacin haihuwarsa a nashi hasahe ya zama 1914 kenan

da wannan maƙalar take da ita da za a bayyana nan gaba kaɗan. Haka nan an tsinci gurun kaza cikin suɗin kwano domin wata rana muna zaman fada a zauren fadar ɗan-Alin Birnin Magaji sai labarin Ɗanƙwairo[4] ya haɗa ni da Ɗanyalla Sarkin Karma / shugaban Dogaran gidan Sarautar ɗan-Alin Birnin Magaji muka tattauna kan Tarihin Ɗanƙwairo Maradun. ɗaya daga cikin abinda na Tambayi Ɗanyalla shi ne, shin ko yana da dangantaka ta jini da Ɗanƙwairo? Sai Ɗanyallan ya ce, "ai waɗannan tarihe-tarihe na gidansu makaɗa Ɗanƙwairo na same su ne daga wajen Mahaifina Muhammadu da Yayana Sulaimanu Ɗandango Sarkin Karma. Sule Ɗandango wanda ya riƙe sarautar daga[5] (1962-1985). shi ne yayan Ɗanyalla (Sarkin Karma 1986-2012). Ma'ana abinda aka samu daga bakin Ɗanyalla ya fito daga bakin mahaifinsa Muhammadu, da ɗan'uwansa Sarkin Karma Sulaimanu Ɗandango. Mahaifin Ɗanyalla Muhammadu yana zuwa wajen wasan Tauri gari-gari har Ɗankadu garinsu Usman Ɗankwanaga mahaifin Ɗanƙwairo. A wajen wasan Tauri ne Muhammadu ya ƙulla abokantaka da Usman Ɗankwanagga makaɗin mayaƙa da 'yan tauri. Muhammadu ya san haihuwar Musa Ɗanƙwairo domin a wata saduwa da suka yi wajen wasan tauri a Ɗankadu ya samu labarin an yi wa Usman Ɗankwanaga haihuwar Musa Ɗanƙwairo wanda a daidai wannan lokacin su Muhammadu suka samu labarin Turawan Ingila sun kawo ziyara Sakkwato cibiyar daular Usmaniyya[6]. Daga wannan hoton lokacin haihuwar Musa Ɗanƙwairo aka fahimci akwai ruwayoyi mabambanta kan lokacin haihuwar Musa Ɗanƙwairo:

i. Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun[7] "shekarun haihuwata 60 daidai yanzu" a wannan tattauna ne Ɗanƙwairo ya ambata tunaninsa kan yawan shekarunsa. Kenan an haife shi a 1914.

ii. Ruwayar Gusau, S. (1996) *Makaɗa da Mawaƙan Hausa* shafi na 104[8] An haifi Musa Ɗanƙwairo Maradun a shekarar 1909

---

[4]. Wanna tattaunawa mun yi ta a ranar 18 /3 / 2000 a bakin fadar Ɗan-Alin Birnin Magaji, bayan wannan kuma na sake isko shi gidansa da ke bakin tsohuwar Kasuwa Birnin Magaji aranar 7 / 5 / 2004 da ƙarfe biyar da yamma.

[5] .Shi Muhammadu mahaifin Ɗanyalla, da Sulaimanu Ɗandago Sarkin karma yayan Ɗanyalla, da shi Ɗanyalla sanannen ɗantauri ne, saboda jarumtakarsa ne har zuwa yau zuri'arsu ke riƙe da sarautar Sarkin Karma na masarautar Birnin Magaji.

[6] . Tattaunawarmu da Ɗanyalla a gidansa da ke bakin Tsohuwar Kasuwa Birnin Magaji kamar a ɗure na 4.

[7] . A shirin Tariihin Makaɗa da Mawaƙa wanda Alhaji Lawal isah ya gabatar a ranar 8/11/1974 a gidan Rediyo Nijeriya na Kaduna

[8] . Gusau, S. M. (1996) *Makaɗa Mawaƙan* Hausa, Kaduna. Fisbas Media Services

iii. Ruwayar Sani, R. (2019) "Nazarin Salo a Cikin Waƙoƙin Alhaji Musa Ɗanƙwairo" Shafi na 56-61[9] ya ambata an haifi Ɗanƙwairo a 1909, amma ya jingina ga littafin Gusau, S. (1996) shafi na 104

iv. Ɗanyalla, Sarkin Karma[10] "A wurin Sarkin Karma Sulaimanu na samu labarin cewa Musa Ɗanƙwairo an haife shi watanni kamin Turawa su kawo ziyara Sakkwato"

Daga bayanan da ke sama za mu fahimci lokacin haihuwar Musa Ɗanƙwairo da ya shiga duhu. Wannan shi ya sa aka ce akwai ra'in fanɗarewa inda saboda rashin ƙwararan hujjoji ko madogara sanin tarihin Ɗanƙwairo ya fara samun ruwayoyi daban-daban, kuma idan ba a daidaita sahun wannan tarihi a yanzu ba, to za a ci gaba da samun ƙaruwar ruwayoyi musamman a lokacin waɗanda suka san tarihi suka gushe a zamansu na duniya.

Tuntuɓe gushin gaba, sai aka turke maganar Ɗanyalla da ɗan waƙar da Ɗanƙwairo ya yi ma Ɗanyalla kamar haka:

**Jagora**: Sarkin taurin Birnin magaji,
**'Yan Amshi**: Ɗanyalla yabo nai mukai,

**Jagora**: Ba Nijeriya kaɗai ba,
Dan nan har ƙasar waje
In dai maganar tauri ce,
**Jagora/'Yan Amshi**: Ko ƙumba ta san Tauri ka kai[11]

Wannan waƙa ta ɗan-Ali Muhammadu Mode Usman ce, amma ɗan waƙar na yabo ne ga Ɗanyalla saboda shi ne mai masaukin Ɗanƙwairo, kuma akwai dangantaka ta iyaye tsakanin iyayen Ɗanyalla da iyayen Ɗanƙwairo a nasu zamanin. Da wannan za a waiwayi tarihin yadda sarakunan |urmawa suka taimaka wa jihadin Mujaddadi Shehu Usman ɗanfodiyo (Allah ya sada shi da rahamominsa amin). Makaɗa Kaka (kakan Ɗanƙwairo) makaɗin Sarakunan

[9] Sani, Alhaji Rabi'u (2019) "Nazarin Salo a Cikin Wasu Waƙoƙin Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun" Kundin Digiri na Biyu, Sakoto: Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo

[10] . kamar a ɗure na 6

[11] . Waƙar Ɗan'Alin Birnin Magaji Alhaji Muhammadu Mode Usman wadda a cikinta ne aka yabi Ɗanyalla mai masabkin Musa Ɗanƙwairo a lokuttan da yake kai yawon kiɗi a masarautar Birnin Magaji.

ƙurmawan Bakura ne. A lokacin yaƙe-yaƙen da waɗannan sarakuna suka yi, Makaɗa yana daga cikin makaɗan yaƙi a wannan lokaci. Haka nan yana yi wa masu wasan Tauri a daji kiɗan tauri. Wajen wannan wasannin tauri ne Makaɗa Kaka ke haɗuwa da Sarakunan Karma na garuruwa daban-daban har da su Muhammadu sarkin taurin masarautar ɗan-Alin Birnin magaji. Wannan bayanin ya ba mu hoton yadda Ɗanyalla yake ƙaunar Alhaji Musa Ɗanƙwairo kuma ya san tarihin iyalan Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun.

## 1.2 Tasirin Ra'in Fanɗara a Cikin Tarihin Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun

A bayanan da za su biyo a cikin babi na biyu da na uku, za a fahimci dalilin amfani da wannan ra'i na fanɗarewa. Domin a bayanan da aka ci karo da su an fahimci manyan abubuwa guda biyu:

i. Musa Ɗanƙwairo ya bayyana shekarunsa, daban da waɗansu mutane waɗanda ke tunanin suna mu'amala da iyayensa, wanda a tunaninsu Musa Ɗanƙwairo bai faɗi shekarunsa daidai ba. Kennan Musa Ɗanƙwairo ya faɗi shekaru daban, wasu sun bayyana abinda suka sani game da shi daban.
Hasashen wannan maƙala shi ne nan 'yan wasu shekaru kuma shekaru ba masu nisa ba, Tarihin haihuwa /Shekarun Musa Ɗanƙwairo za su shige duhu a hannun mutane har mai yiwuwa ya kasance masu son gina tarihi su shirya tarihin Musa Ɗanƙwairo bisa nasu hasashe wanda zai yi nisa da gaskiya. Yana iya kasancewa waɗanda suka san Musa Ɗanƙwairo ba su nan a wannan duniya ta mu, ko sun tsufa ko wasu lalurori makamantan hakan da kan kasance ga mutane, waɗannan na daga cikin dalilan da suka sa wannan maƙala ta yi wannan has ashen ganin sauran iyalan Musa Ɗanƙwairo suna raye, waɗanda suka san shi suna raye, masu nazari a kansa suna raye, amma ga ruwayoyi nan mabanta kan shekarun haihuwarsa sun samu wanda illa ne ga tarihi. Kuma ya kamata masu nazari kan Musa Ɗanƙwairo su himmatu wajen tabbatar da tarihin Musa Ɗanƙwairo na gaskiya.

ii. Waƙoƙin Alhaji Musa Ɗanƙwairo suna son su fara ɓacewa a hannun jama'a. An kawo wannan magana saboda a lokacin da nake neman wasu waƙoƙin da ba ni da su a lokacin da nike talittar wannan maƙala, sai mamaki ya kama ni kan cewa babu wasu waƙoƙin a hannuna, babu waƙoƙin a kasuwa wajen masu sayar da kaset-kaset, babu waƙoƙin a hannun 'ya'ya da jikokin waɗanda aka yi wa waƙoƙin, babu waƙoƙin a gidajen rediyo da ma'aikatun watsa labarai. Amma na samu wasu waƙoƙin a hannun abokaina da kuma masu sauraren waƙoƙin Ɗanƙwairo Maradun.

> Kamar yadda na bayyana a sama, idan sauran iyalan Musa Ɗanƙwairo suna nan raye, idan akwai hanyoyin sadarwa na zamani da ake amfani da su wajen sake adana duk wata fasaha da ke a baka ko a kasetko a garmaho, kuma akwai gidajen sarautar da Musa Ɗanƙwairo ya yi ma waƙoƙi, kuma aka samu wannan tsaiko kan samun wasu waƙoƙi na ɗanƙwaio, to lallai ya kamata mu farka daga baccin da muka fara yin a barin tarihi ya salwance a hannummu. Mafita shi ne, irin wannan tattaunawa a rana mai kamar ta yau, ta zamar mana wa'azi.

Da wannan bayani dake sama (na hasashe na) nan emo ra'in fanɗarewa domin in nuna yadda da-sani za mu yarda tarihin rayuwar Musa Ɗanƙwairo musamman shekarusa na haihuwa zai shiga ruwaice-ruwaice. Haka nan muna zaune dandaras, waƙoƙinsa za su fara salwancewa[12]

Naɗewa

Babi na gaba wato na biyu da na uku zai zo da bayani kan ruwayoyin shekarun Musa Ɗanƙwairo, da matsayinsa a duniyar waƙa. A cikin naɗewar wannan babi na farko zan aro ɗaya daga cikin ɗiyar waƙar Musa Ɗanƙwairo kamar haka:

> **Jagora**: Ga wata rigima bana,
>
> **Jagora/ 'Yan'amshi**: ba ƙare ta bar aba,
> **'Yan'amshi**: Mutum huɗu da zane ɗaya,
> Sunan nan shigihwa ɗaya,
> In za a yi kwanciya,
> Sai dai a raba huɗu,
> Ko kuma a yi yamutci,
> *Turken Waƙa: Shiryayye Makaye, ɗan Garba na Garkuwa*

[12] . Gusau, S. M. (2019) ya shirya *Diwanin Waƙoƙin Baka Juzu'i na Huɗu* Wasu Waƙoƙin Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun (1909-1991) Sarkin Kiɗan Sarkin Maradun Jihar Zamfara wato kundi mai ɗauke da waƙoƙin Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun, kuma ya yi wani irinsa kan Waƙoƙin Mamman Shata Katsina. Wannan gagarumar gudummwace ga adabin Hausa, kuma idan da za a ci gaba da yin hakan, da an taya Farfesa Sa'idu Gusau ceto tarihin waɗannan mashahuran mawaƙa da fasahancinsu daga salwancewa.

Wannan ɗan waƙa daga cikin waƙar sarkin ƙayan Maradun Ibrahim Maigandi II wanda ya yi sarauta 1981-2003. Inda Ɗanƙwairo ya bayyana a cikin ɗan waƙa cewa gidan Alhaji da gidan Attahiru  su ne ɗiyan Mu'alleɗi Sarkin Ƙayan Maradun na farko daga zuriyar Fulani Torankawa wanda ya yi sarauta daga 1870 zuwa 1874 ne. Wannan sarauta ta zama gidaje biyu ke gadonta. Ana ta rigingimu wajen zaɓen sarkin da ɗare karagar mulki. Rigimar samun sarautar kan lafa idan wani ya samu zama sarki, amma ba don rigimar ta mutu ba, takan taso idan sarautar ta sake faɗuwa, sai a ci gaba ko kuma wata sabuwa ta ɓullo.
Ga tarihin shekarun Musa Ɗanƙwairo ya shige duhu ba samu mafita ba, ga kuma na waƙoƙin gidajen sarakuna sun fara salwanta, sa'annan ba a ko binciki wasu waƙoƙin da ya yi ma jama'a ba, da waƙoƙi noma waɗanda nan ne ya gwada fasaharsa ta farko a waɗe ba.

## 2.0 Wane ne Musa Usman Ɗanƙwairo Maradun?

Musa Ɗanƙwairo sanannen mawaƙi ne wanda ya rayu a ƙasar Zamfara ta arewacin Nijeriya a ƙarni na Ashirin 20[13]. Iyayen Musa Ɗanƙwairo mawaƙan baka ne, saboda shi a wajensa ɗangado ne ba hayen waƙa ya yi ba. Ana iya cewa bayan sanayyar Ɗanƙwairo kan waƙa, shahararre ne a ta fuskar waƙoƙin Noma da Sarauta da kuma Masu-Gari (Jama'a). Wanda ya yi tashe ga yin waƙoƙin babbar Sana'a ta Noma da Sarauta da Sarakuna da kuma manyan mutane, to *La-Shakka* sunansa dole ya zama tamkar ***Tambari a ji ka Sama'u***. Tarihin makaɗa da mawaƙa na lokacinsa ba zai cika ba, ba tare da ambaton sunansa ba.

## 2.1 Sanin Musa Ɗanƙwairo daga Bakinsa

Musa Ɗanƙwairo ya gadi fasihancinsa ne ga Kakansa (Makaɗa Kaka) da Mahaifinsa (Usmanu Ɗankwanaga). Shi da kansa yana bayyanawa a ɗaya daga cikin waƙoƙinsa kamar haka:

**A. Jagora**: Batun Kiɗi,
Ko ba ku nan yi mukai,
Kun karantar da mu,
Mun yi ƙidan baƙi,
Mun yi wasilla,
Mun yi ta yi,
Yanzu ilmi mukai tunda mun sabka,
In hwa waƙa ta,
Don mun san yadda za mu ƙulla ta,

**Jagora/'Yan'amshi**: In an ce mutum mai tujara ne,
Sai ya haihwa ɗa mai tujarannan,

**Jagora:** in an ce mutum ga shi samna ne,
**Jagora/'Yan'amshi**: Sai ya haihwa samna haƙiƙan ne,

**Jagora:** In Allah ya wa mutum ƙwazo,
**Jagora/'Yan'amshi**: Ya bah haihwa ɗa nai ya lalace,
Tun da gado ne
**Jagora:** Mun gani tun ga ɗiyan Masara,
**Jagora/'Yan'amshi**: Ga abu goye kowa da gemu nai,
***Gindi Waƙa*** *Shirya Kayan Faɗa mai gida Tcahe,*
*Ali ɗan Iro baka ɗauki reni ba*[14]

[13] . Za a ga ratayen tattaunawar da aka yi da Ɗanƙwairo kan tarihin rayuwarsa da kiɗe-kiɗensa a ranar 8/11/1974 wanda gidan rediyo Nijeriya na kaduna suka yi da shi a shirin makaɗa da mawaƙa. Rataye na 'A' na wannan maƙala

[14] . Waƙar 'Yandoton Tsafe Alhaji Aliyu, an naɗe wannan waƙar a gidan Rediyon Rima da ke Sakkwato 20 ga watan Apirilu 1995, a lokacin ina aiki a gidan rediyon a matsayin jami'i mai farauto labarai.

A ɗan waƙar da ke sama Musa ɗan ƙwairo ne ke bayyana kansa ta hanyar danganta fasaharsa da ta kakaninsa. Ya yi amfani da salon siffantawa inda ya kawo hoton rabon mutane a cikin al'ummarsa da ɗiyan masara wadda bututunta tana goye da ɗiya da yawa, amma kowane dan masara yana da wasu zaruruwa tamkar gemu. Wato wannan misali na ɗiyan masa sai aka danganta shi da mutane a matsayin al'umma ɗaya amma kowa da halayyarsa. Misali akwai mutanen da halayyarsu ta tujara[15] ce, wasu kuma samnoni ne, wasu kuma lalatacci ne, wasu kuma masu ƙwazo[16] ne. magabatan Musa Ɗanƙwairo tun daga kakaninsa (waɗanda bayanai za su zo nan gaba kaɗan) cewa su masu ƙwazo ne, saboda haka da bazar magabatansa yake ta rawarsa domin ***ɗan-na-gada ne.***

(B) **Jagora:** Mai kyauta da jikkuna,

**'Yan'amshi**: Da Dawaki da riguna,
Jikan Shehu ɗan Hassan,
Sardauna Firimiya,
Yau kai adda duniya,
Duk abi kyauta Allah ya saƙaƙe maka,
*Don batun* ***magana*** *sai ƙwairo mai toho,*

**Jagora**: Ubangiji ya zuba ma albarka,
**'Yan'amshi:** Kwamishinan lardin Sakkwato ya kyauta,
**Jagora:** Dallatun Zazzau,
**'Yan'amshi**: In gai sai tilas ne,
**Jagora:** Madawaki mu gai sai,
**'Yan'amshi:** Don ya kyautat man,
**Jagora:** Sarkin Kudu ɗan zaki,
**'Yan'amshi:** Ko shi ya kyauta man,
***Gandin Waƙa*** *mai dubun Nasara garnaƙaƙi Sardauna. Ba a hau maka barde shi aw wargaiga)*[17].

[15] . Mutum matujarci yana nufin mafaɗaci, mai yawan satiru, da yajin magana a maimakon magana ta ladabi da lumana. Mai tujara yana iya zama hatsabibi wanda ba ya son zaman lafiya.

[16] . Mutum mai ƙwazo ana kallonsa da matsayin Gwarzon mutum abin alfahari ga al'umma gaba ɗaya. Mai ƙwazo ba samna ba ne ba malalaci ba ne. Musa Ɗanƙwairo ya danganta magabatansa da masu ƙwazo.

[17] . Waƙar Sardaunan Sakkwato, Firimiyan jihar Arewa, Sir Ahmadu Bello, an naɗe wannan waƙar a studiyo na ma'aikatar yaɗa labarai ta jihar Sakkwato a ranar 30 Yuli, 1994.

A ɗan waƙar da ke sama Musa Ɗanƙwairo ya bayyana kansa a cikin wani salo na Abantarwa da mawaƙa ke amfani da ita a matsayin wata hikima ta waƙa. Wannan salo shi ne na ɗaukar wata halayya ta abinda ba mutum ba, a danganta shi da abu mai rai, ko a danganta shi da mutum. Misalin haka shi ne kalmar toho da ta keɓanta ga tsirrai musamman itace/ice. Ice shi ne yake yin tsiro, a wata kalma ana cewa icce ya tofa/toho/tofo. Mutum haihuwa yake yi a maimakon tohon da icce ke yi. Idan ice yana tofowa, yabanyarsa tana yawaita ta yi kyau gwanin ban sha'awa har dai a lokacin damana inda za a sababbin kunnuwa da rassan icce suna ƙara tsawo,icce yana kakkaɓe tsofaffin kunnuwansa sababbi suna hitowa suna rausayayawamusamman idan iska yana kaɗawa. Irin wannan yanayi na itace shi kan samar da inuwa mai sanyi da mutane ke zama a ɗarƙashin inuwar itacen suna shan iska suna hutawa. Ba mutane ba har dabbobi suna kwantawa a ɗarɗashin irin waɗannan itace suna hutawa da rage raɗaɗin zafin rana.

Da wannan hoton ice mai toho Musa Ɗanƙwairo ya bayyana kansa, da matsayinsa a cikin al'ummarsa.

(C) **Jagora:** Ga wata waƙa nan na shirya,
Yara ku ɗau niyyaƙ ƙarawa,

**'Yan'amshi**: ***ƙwairo malamin waƙa***,
In ka wallafa littafi,
In ka ba mu sai mu karanta,
Shi noma nai alheri,
Mu ko noman mu waƙa,
Kowa ya tsare hanyag gadonai,
Mamman Jikan Abdu,
Gagaru ƙarya mai ban tsoro,

***Gindi Waƙa**: Gagara ƙarya mai ban tsoro, Mamman Jikan Abdu*[18].

ɗan waƙar da ke sama a nan ma Musa Ɗanƙwairo ya bayyana kansa da cewa shi malamin waƙa ne. Malami a kowace al'umma matsayinsa babba ne. A ƙasar Hausa inda ma fi yawan Hausawa musulmi ne, ana kallon malamai da magada Annabawa. Annabawa kuma su ne Allah Ubangijin talikai ya aiko zuwa ga mutane da saƙonnin yadda za su bauta masa. Haka nan Malamai su ne waɗanda suke da tarin ilmin da suke gabatarwa ga sauran al'umma domin su jagorance su bisa kiyaye dokokin Ubangijinsu. Musa Ɗanƙwairo shi kuma malami ne amma ta fuskar waƙar baka, inda yake lurassuwa da kira ga al'umma a cikin siga ta nishantarwa domin su tafiyar da rayuwarsu bisa hanya madaidaiciya, tamkar malami mai wa'azi da ayoyin Al'qur'ani.

(D) **Jagora**: Dum makaɗanda at tcahe nai jam'i,
Hab baƙi har 'yan gidan su duka,

**'Yan'amshi:** ***Babu mai ƙulla waƙa kamat tawa***

**Jagora:** Ga makaɗi ya shirya waƙa tai,
Sai a amsa mashi ba a ƙara mai,
***In niƙ ƙulla waƙa a ƙara man,***
***Mu haɗu duk azanci garemu,***

**'Yan'amshi:** ƙaaƙa mutun guda za ya raɗɗe mu?
Shirya kayan hwaɗa mai gida Tsahe,
Ali ɗan Iro baka ɗauki reni.

[18] . Waƙar Sarkin Daura Alhaji Muhammadu Bashar, an same ta kamar a ɗure na 16 sama.

*Gindin Waƙa: Shirya kayan hwaɗa mai gida Tcahe Ali ɗan Iro baka ɗauki reni ba*[19].

A nan Musa Ɗanƙwairo ya bayyana ƙarara cewa ya fi sauran makaɗan da ke yi wa 'Yandoton Tsafe waƙa azanci. Ya ƙara da cewa shi da yaransa na waƙa duk masu azanci ne, da sauran mawaƙa sai dai su biyo bayansu a cikin fasahar waƙa.

## 2.2 Sanin Musa Ɗanƙwairo Daga Bakin Wasu Makaɗa

ƙarƙashin wannan taken, za a ga matsayin Musa Ɗanƙwairo a duniyar waƙar baka, da a idon duniyar Hausawa ta fuskar waƙa. Kowane mawaƙi yana da masoyansa a cikin sana'arsa, kuma ba zai rasa abokan kaukawa / kokowa ba. Ta sanin hakan ne a ga sanin Ɗanƙwairo ta bakin wasu mawaƙa yana da amfani. Ga misali waƙoƙin wasu makaɗan kamar haka:

(A) **Jagora**: Wannan zamani na ne,
Yau tauraruwa ta ce,
Ba mai roƙon manoma ba,
Ba mai roƙo ga mata ba,
Ga nanniya ko Sarki zaka roƙo,
Ba ƙarya bace ko Narambaɗa,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba,

Jagora: Maidamma,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba.

Jagora: Had damman,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba,

Jagora: Wa Galadi,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba,

Jagora: Har Tswaga,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba ,

Jagora: Isah Makaho,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba,

Jagora: ɗan kyana,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba,

[19] .Waƙar 'Yandoton Tsafe Aliyu II , na samu wannan waƙar ne daga hannun abokina Alhaji Abdullahi Maikano Wudil ranar 17 / 02 / 2019

Jagora: ***Ɗanƙwairo***,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba,

Jagora: ***Haƙ ƙwairon***,
**'Yan'amshi**: Ya san akwai Garba
***Turken Waƙa***: *Ba rana jiki, a riƙa mu gani haka nan an ka san aiki*[20]

Makaɗa Garba ɗanduddu ya fitar da jerin makaɗa da mawaƙa waɗanda a wannan lokaci su fitacci ne. Zamanin da ɗanduddu ya yi wannan waƙar, babu fitaccin da suka fi su ɗan-Kyana da Isah ɗanmakaho da Ɗanƙwairon. Saboda ɗadduddu ya nuna ya san zuri'ar gidansu Ɗanƙwairo da shahararsu a fagen waƙa sai y ace ba Musa Ɗanƙwairo ba, har ma kawunsa ƙwairo wanda ake yi ma Ɗanƙwairo inkiya da sunansa, to ya san da zaman ɗanduddu mai waƙa. Kenan a zamanin ɗanduddu, sunan makaɗa ƙwairo da Kurna sun yi tashe a fagen waƙa.

(B) **Jagora**: Kaico zamani zo mu tafi,
Zamani ina zaka da mu,
Kaico zamani zo mu tafi,
Zamani ina zaka da mu,

Gaugawa ba ta kunu,
Dole ne a daure ya nina,
Ina gaida Haja da Amina,
Matan muhamman na Abu.

Yau ina ɓarayin waƙa,
Masu sace waƙan mu su yi,
Yau tsaya mu lissafa ma,
Masu ƙulla waƙa ta tafi,
Ko'ina ka gane su daban,
Ba mu san manyammu ba,
Don manya manya layinsu daban,
Don manya manya layinsu daban,
Kamar su Alhaji Shata,
Ba mu sa su layinsu daban.
**Kamar su *Alhaji ƙwairo*,**
**Ba mu sa su layinsu daban**
***Gindin Waƙa:*** *Kaico Zamani zo mu tafi,*

---

[20] . Wannan waƙa ta Makaɗa Garba [anduddu Gangara ce, gundumar Kuryar Dambo a yankin ƙasar Shinkafi, wadda a yanzu ke a jihar Zanhwara. Ya yi wannan waƙar a tsakanin shekarun 1970 zuwa 1980, na samu wannan waƙar a hannun Alhaji Abdullahi Mohammed da ke Birnin Magaji da ke jihar Zamfara, ranar 2/11/2007

*Zamani ina zaka da mu*[21]

Fitaccen fasihinnan Sani Sabulu ya bayyana cewa Makaɗa Musa Ɗanƙwairo yana daga cikin manyan mawaƙan ƙasar Hausa, saboda haka shaguɓen da yake yi wa wasu mawaƙa masu satar fasahar su Sani Sabulu suna rerawa domin samun suna da ɗaukaka a fagen waƙar to su sani cewa an gano su. Amma su su ƙwairo ba su daga cikin waɗannan mawaɗan don su manyan mawaƙa ne.

(C) **Jagora**: Daura ni kai in ishe Sarki,

**'Yan'amshi**: Mamman Bashar mai hana ƙarya,
Dattijo bai san wargi ba,
Mamman Bashar mai hana ƙarya
Dattijo bai san wargi ba,

**Jagora:** Mutane ya kamata mu je Daura,
Don na ji Shata na ta faɗi,
***Danƙwairo Dottijo na ta faɗi***,
Sun ce Bashar na raba mota,
Sun ce Bashar na raba kuɗɗi,

**'Yan'amshi**::Ai sani ba an ce na ba,
Ko wa ishe Baba gari nai,
Mutun na sanin ba a yi ƙarya,
Daura ni kai in ishe Sarki,
Mamman Bashar mai hana ƙarya,

Gindin Waƙa: Daura nikai in ishe Sarki, Mamman Bashar mai hana ƙarya, Dattijo bai san wargi ba[22].

Shi kuma Makaɗa Aliyu ɗandawo ya bayyana Ɗanƙwairo da Dattijo. Dattijo kuma wani matsayi ne na daraja da mutum ke samu saboda halayensa na kirki da kamala da yake da su, ko ya nuna a cikin al'umma.

[21] . Makaɗa Sani Sabulu Na-Kanoma a waƙarsa ta Zamani zo mu tafi. Na samu wannan faifan waƙar a hannun Alhaji Sani Sabulu shi da kansa, a wata haɗuwa da muka yi a garin Talatar Mafara jihar Zamfara a ranar 23 / 09/ 1998

[22] . Waƙar Mamman Bashar Sarkin Daura, ta Makaɗa Sani Aliyu [andawo wadda aka shirya a garin Sakkwato ranar 5/2/1993 a shiyyar minannata gidan Marigayi Alhaji Ummaru Abacha.

**2.2.1 Waƙar Sarkin Burmin Bakura (ana neman burbushin Jaruntaka a cikin waƙoƙin waɗannan Sarakuna waɗanda makaɗa Kaka mai ganga Ɗankadu yayi wa waƙa)**

Burmawa a tarihin Zamfarawa tafiyayyu ne[23], Burmawan Bakura suna danganta kansu daga ƙasar Kanuri ta yankin Borno. Daular Mai wadda take kai yaƙin faɗaɗa daularta, ya sa wasu daga cikin jama'ar Borno suka yo yammaci suka roƙi wurin zama daga Sarkin Zamfara na wannan lokacin ya ba su Bakura suka zauna. Ana kintatar shigowar waɗannan Jama'ar da suka fara zama Bakura a shekarar 1756[24]. Burmawa sun taimaka wa malaman jihadi, kuma Sarakunan Burmawa suna da makaɗan da suke gwarzanta su kamar Makaɗa Kaka Ɗankadu Bakura

| | |
|---|---|
| (A) **Jagora**: | Ya yi damben girma Isihu,<br>Bawan S/Musulmi, |
| **'Yan'amshi**: | Ya yi damben girma Isihu,<br>Bawan S/Musulmi, |
| **Jagora**: | Malam na Sansani jikan ɗanƙwai, |
| **'Yan'amshi**: | Mai ƙudurin kwana da ƙwazo,<br>Yayo damben girma Isihu,<br>Bawan S/Musulmi, |
| **Jagora:** | Ko da ƙarhi ba a ima, |
| **'Yan'amshi:** | Toron Giwa sai hasashe,<br>Toron Giwa sai hasashe,<br>Yayi damben girma Isihu,<br>Bawan S/Musulmi, |
| **Jagora:** | Ko gobe gidan Ima addamu,<br>Dag ga Ima sai Yahaya, |
| **'Yan'amshi:** | Yanzi Isihu ka mulki,<br>ƙulli in na Allah ne,<br>Wane mutun ya kwantai, |
| **Jagora/'Yan'amshi**: | Wagga fansa ba ta ɗauki,<br>Yara ku ɗau dangana,<br>Yan uba kuma sai takaici, |

[23] . Ibrahim, A. T. (BS) Facinating Emirates of Zamfara State of Northern Nigeria, shafi a 15-22

[24] Kamar ɗure na 22 a waƙar Mamman Sarkin Daura

Ya yi damben girma isihu,
Bawan Sarkin Musulmi,

***Gindin Waƙa****: Ya yi damben girma Isihu, Bawan Sarkin Musulmi*[25]

Wannan waƙa ta Musa Ɗanƙwairo ce wadda ya yi wa sarkin |urmin Bakura II wanda yai sarauta (1960-1970) ƙumshiyar wannan waƙa ta naɗe tarihin irin yaƙin da ya hwaru tsakanin sarakunan |urmawa da sarakunan Zamfara waɗanda ba su ba malaman jihadin daular Usmaniyya hadin kai ba[26].

**2.3 Sanin Musa Ɗanƙwairo a Ruwayar Manazarta** Manazarci zai iya gano fasihanci da basirar ɗankwairo daga Kakansa Makaɗa Kaka mai ganga Dankadu ta hannun mahaifinsa Usman Kaka ɗanadau, ta renon yayansa Makaɗa Kurna Usman

A. Fafesa Sa'idu Gusau
“Alhaji Musa Ɗanƙwairo makaɗi ne da ya gaji magabatansa a kiɗan fada, kuma ya riƙi Sarauta, ta sarkin kiɗan Sarkin ƙayan Maradun, kuma har wayau bai taɓa kauce wa manufofi da sigogin kiɗan fada ba, ashe ya cancanci a kira Musa Ɗanƙwairo Makaɗin Baka na fada”[27]

B. Malam Sani Alhaji Rabi'u
Tun bayan da Musa ya kai kimanin shekara bakwai,
Sai ya soma karɓI tare da mahaifinsa,
saboda yana da zaƙin murya kamar ƙwairo,
Sai Usman (mahifin Musa), y ace “Ga ƙwairo na biyu kuma an mayas”

---

[25] . Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun ne ya kwaikwayi salon waƙar makaɗa Kaka mai ganga [ankadu a lokacin da yake rera ma Sarkin Burmin Bakura Alhaji Yusuf na II waƙa. Na samu wannan waƙar a hannun Alhaji Musa Ɗanƙwairon da kanshi a wani lokaci da na kai ziyarar aiki domin tattaunawa da shi kan waƙarsa da ya yi a kan Dam na Bakalori a ranakun 4 da 5 na watan Disamba 1985 a gidansa da ke gidan Kano da ke Maradun jihar Zamfara.

[26] . An samu wannan bayani a littafin *Infaƙul Maisuri* : Taƙaitaccen Tarihin {asashen Tukururu na Sarkin Musulmi Muhammadu Bello, fassarar Sidi Sayuɗi da Jean Boad, 1974, shafi na 99

[27] . Gusau, S.M. (1988) Waƙoƙin Makaɗan Fada: Sigoginsu da Yanaye-yanayensu. Kundin Digiri na Uku: Kano Jami'ar Bayero, shafi na 170-177

*Fara Waƙarsa*

Alhaji Musa Ɗanƙwairo ya fara koyon kiɗa a wajen mahaifinsa tun yana ɗan shekara bakwai, watau wajajen 1916. A lokacin ya soma da kiɗan kanzagi ne har ya zo ga karɓi, kamar dai yadda ake fara koyon kiɗa. mahaifinsaya hannunta shi ga yayansa Abdu Kurna. ***A wurin Abdu Kurna ya naƙalci kiɗaSosai[28].***

Naɗewa

A kowane muhalli, akwai kalmomin da ake tantance matsayin mutum da su. Idan Hausawa suka zaɓi kalmomi wajen bayyana mutum kamar a ce wa mutum raggo, malalaci, maƙaryaci, wawa ko mai wauta, ƙazami, dolo, gaula ko marar wayau, to wannan mutum / rukunin mutane da ake dangata su da waɗannan kalmomi ba mutane ba ne da al’umma ke alfahari da samunsu ba. Ba su da wata gudummuwa da suke bayarwa ga ci gaban kansu da iyalansu da kuma al’umma ga baki ɗaya. A ɗaya ɓangare, in aka ce wa mutum Dattijo, mutumin kirki, mai ƙwazo, fasihi aka ƙara da kiransa malami; to iyakar kamala ta samu ga wannan bawan Allah.

A wannan babi wanda ya bibiyi yadda Alhaji Musa Ɗanƙwairo ya yi ma kansa mazauni a muhallin waƙar baka, da yadda ‘yanuwansa mawaƙa suka yadda da zamansa jagoransu a fannin waƙa, an samu damar cewa, Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun Madugu ne uban tafiya (a zamaninsa) a cikin ayarin mawaƙan ƙasar Hausa.

[28] . Sani, A. R. (2019) “Nazarin Salo a Cikin Wasu Waƙoƙin Musa Ɗanƙwairo Maradun”, Kundin Digiri na Biyu, Usmanu [anfodiyo, Sakkwato, shafi na 57-62

## 3.0 Babi na Uku: ƙasar Zamfara a Bakin Musa Ɗanƙwairo

Alhaji Musa Ɗanƙwairo makaɗin noma ne, makaɗin jama'a ne, sannan makaɗin Sarakuna ne. Iyalan Musa Ɗanƙwairo (magabatansa) sun kiyaye da hazaƙarsa ta fuskar waƙa, saboda haka suka fara daidaita sahun tunaninsa a kan ya fara yi wa sarakuna waƙa. Waƙar da Musa ɗanƙairo ya fara yi ma Sarakuna ita ce ta Sarkin 'Yandoto Aliyu.[29]; daga nan fa Alhaji Musa ya ci gaba da gwada baiwarsa ga Sarakai da hakimai kamar haka:

### 3.1 Sarkin Zamfaran Anka

Jagora: Muhammadu mai gida Anka,
ɗan Usmanu ɗan Abdu,
'Yan'amshi: Muhammadu maigida Anka,
ɗan Usmanu ɗan Abdu,
Jagora: Ya yi kokuwa ya tausge maza,
'Yan'amshi: Ya taushe cikinsu wasu na,
Jagora: Manyan Sarakuna na ƙasar Hausa,
'Yan'amshi: Ku an ka sani na tun hwarin,
*Turken Waƙa: ɗan Usmanu ɗan Abdu Muhammadu Mai Gida Anka*[30]

### 3.2 Sarkin Talatar Mafara

Jagora: Muhammadu kai ne Jigigi kai ne,
'Yan'amshi: In yag gane ka ya san kai ne su,
Mai martabarsu na nan hannunka
Gindin Waƙa: Kak ka yarda a rena ma,
Sarkin Mafara Babban Dodo
Jagora: Wandara taho da shirin yaƙi
'Yan'amshi: Jikan na ku ci babban dodo
Kak ka yarda a rena ma
S/Mafara babban dodo
Jagora: Kiɗin milki sai ɗaƙwairo,
Kakannin mutum nika hwaɗi,
'Yan'amshi: Bani kame-kame ga waƙa ta,
Jagora: Kowas san Sarki Barmo,
'Yan'amshi: In ya gane ka ya san kai ne shi,
Jagora: Kowas san Sarki Umaru,
'Yan'amshi: In yag gane ka ya san kai ne shi,
Jagora: Kowas san Sarki Aliyu,

[29] . Waƙar 'Yandoton Tsafe, Alhaji Aliyu Mai Turken Waƙa "*Bi da arna bai yarda a kai mai wargi ba, mai wuyag gaba ya hana ƙarya 'Yandoto*" ita ce waƙar Ɗanƙwairo ta Fada/sarauta/Mulki ta farko. Ya yi wannan waƙar a shekarar 1960. Ɗanƙwairo da kansa ya shaidar da haka a ranar 8 / 11/1974, cikin tattaunawar da Alhaji Lawal Isah ya yi da shi a gidan rediyon Nijeriya na Kaduna.

[30] . Waƙar Sarkin Zamfaran Anka, Muhammadu Lauwali, na saurari wannan waƙa daga kaset na Rikoda, a ranar 7/3/1997. Bayan Saurare na shifce wannan waƙar domin yin nazari a lokutta daba-daban.

‘Yan’amshi: In yag gane ka ya san kai ne shi
Jagora: Kowan san Sarki ɗanbaƙi
‘Yan’amshi: In yag gane ka ya san kai ne shi
Jagora: Kowas san Sarki ɗangwanno
‘Yan’amshi: In yaggane ka ya san kai ne shi
Jagora: Kowas san Sarki ɗangwanno
‘Yan’amshi: In yag gane ka ya san kai ne
Jagora: Kai aj Jigigi kai ne Jiga
‘Yan’amshi: In yag gane ka ya san kai ne
Jagora: Muhammadu kai ne Jigigi kai ne Jigara
‘Yan’amshi: In yag gane ka yasan kai ne su
Martabarsu na nan hannunka.

*Turken Waƙa: Kak ka yarda a rena ma, Sarkin Mafara babban Dodo*[31]

### 3.3 Sarkin Dankon Bukkuyum

Jagora: Ka da ka ɗau reni
Junaidu ya wuce reni mai sulke
‘Yan’amshi: Kada ka ɗau reni
Junaidu ya wuce renin mai sulke
Jagora: Kai aɗ ɗan Jibo
‘Yan’amshi: Kai a Abubakar ka wuce wasa
Kada ka ɗau reni
Junaidu ya wuce reni mai sulke
Jagora: Junaidu Uban Babangida
‘Yan’amshi: Mai rabo da yawa namijin gaske
Kada ka ɗau reni
Junaidu ya wuce reni mai sulke
Jagora: Ba a zuwa Bukkuyum yaƙi
‘Yan’amshi: Ba a zuwa zaki na nan
Ko dole ba su zuwa zaki na nan
Ka da ka xau reni
Junaidu ya wuce reni mai sulki
Jagora: Sarki ɗan Sarki jikan Sarki
Mai Nasarawa mai Bukkuyum
Mai Gurusu da Gwashi
‘Yan’amshi: Kai ad a Birnin zarumai
Kada ka ɗau reni
Junaidu ya wuce reni mai sulke

[31] . Waƙar Sarkin Mafara, Talatar Mafara, Alhaji Muhammadu Barmo. Na samu wannan waƙa a wajen Alhaji Aminu Mai Kaset Talatar Mafara a ranar 2 / 8 / 2002.

*Turken Waƙa: Kada ka ɗau reni. Junaidu ka wuce reni mai sulke* [32]

**3.4 Sarkin Kwatarkwashi**

Jagora: Ya daka ma arna kashi,
'Yan'amshi: Masu kirkiza dus sun bi,
Sha da arna babban dodo,
Jagora: Manyan maza na Ummaru,
'Yan'amshi: Kwatarkwashi kware sai zagi,
Ya daka ma arna kashi,
Masu kirkiza dus sun bi,
Sha da arna babban dodo,

*Turken Waƙa: ya daka ma arna kashi, masu kirkiza dus sun bi, sha da arana babban Dodo*[33]

**3.5 'Yandoton Tsafe,**

Jagora: Bida arna bai yarda akai mai wargi ba
Mai wuyag gaba ya hana ƙarya 'Yandoto
'Yan'amshi: (Kamar a sama, na Jagora)
Jagora: Ya hau da Lahiya
'Yan'amshi: Sabka Lahiya Uban S/ƙofa
Ci maraya Dodo wandara gwarzon sani
Bida arna bai yarda akai mai wargiba
Mai wuyag gaba ya hana ƙarya Yandoto
Jagora: Naɗa mani S/kiɗI na Jekada
'Yan'amshi: Mui ta duniya kurna na ga S/ƙaya
Ɗanƙwairo makaɗin Yandoto
Bida arna bai yarda akai mai warg
Mai wuyag gaba ya hana ƙarya yandoto

Waƙar Yandoton Tsafe, Alh. ALiyu Mai Gindi Bida arna bai yarda akai mai wargi ba Mai wuyag gaba ya hana ƙarya Yandoto.

Wannan ita ce waƙar Ɗanƙwairo ta Fada/Sarauta/Mulki ta farko. Ya yi ta a shekarar 1960.

*Turken Waƙa: Bida arna bai yarda akai mai wargi ba mai wuyag gaba ya hana ƙarya Yandoto* [34]

---

[32] . Waƙar Sarkin Dankon Bukkuyum, Alhaji Junaidu Adamu. Na samu wanna waƙar a wajen ƙanen Sarkin Sarkin Dankon Bukkuyum Ciroman Bukkuyum Honorabul Abubakar Adamu Bukkuyum, na samu waƙar ranar 18 /11/1993

[33] . Waƙar Sarkin Kwatarkwashi, Alhaji Ahmad Umar mai Kwatarkwashi. Na samu kaset na rikoda na wannan waƙar a shekarar 7/8/2000 hannun Alhaji Adamu Abu Gidan-Zalla, Tsohon Daraktan Hukumar Kula da Al'adun Gargajiya ta Jihar Zamfara

[34] . Waƙar 'Yandoton tsafe, kamar a ɗure lamba ta 1.

### 3.6 Sarkin Zamfaran Zurmi

.

Jagora : Alhaji Allah sa ka gama lafiya,
'Yan'amshi : Alh. Allah sa ka gama lafiya
S/Zamfara Mainasara
Ɗ/Mamman namijin duniya,
Jagora : Ɗauki halin Ummarun Mamuda
'Yan'amshi : Kak ka bari a gwada tsura
Jagora : Da ka zaka sa'ar ana yaƙi ne
'Yan'amshi : Da hana arna motci ka kai
Jagora : Kai an Namoda kai as Sambo
'Yan'amshi : Kunkuru na kai ne a Issau
S/Zamfara Mainasara
Jagora : Ya yi sarauta ya fashe haushi
'Yan'amshi : Ƙauye da birni so nai akai
Jagora : Toron Giwa mai ban tsoro
Zaki kahi gaban reni
'Yan'amshi : Kowah hwarma ka kare mai
Wuya
S/Zamfara Mainasara
Ɗ/Mamman namijin duniya.

*Turken Waƙa :Ɗan Mamman namijin duniya*[35].

### 3.7 Waƙar ɗanmalikin Gabake a Masarautar ƙauran-Namoda

Jagora: ɗan Garba ci da ƙarfi Uban Jakada
Ya wuce gardama
'Yan'amshi: ɗan Garba ci da ƙarfi Unam Jekada
Ya wuce gardama
Jikan Musa ɗanmaliki
Gamda aren Amadu
Jagora: Na S/Kiyawa Dodo ka ke
'Yan'amshi: Wandara ba a gwada matsura
Jagora: Na S/kiyawa mai martaba
'Yan'amshi: Wandara ba a gwada matsura
Jagora/'Yan'amshi Wanda duk yaj jaka bugu na
Baura wanda duk yay jaka buginai kaka
Jagora: Halin ɗanmaliki kutunku
'Yan'amshi: To shi ne Baura yariƙa
To shi ne Baura yarriƙa

[35] . Ɗanƙwairon Kaduna ne (Alhaji Lawal Daudu) ya ba ni wannan waƙar ranar 25/08/2021.

Jagora: Dud ɗanmalikin da an kayi Gaba
'Yan'amshi: Dag gare ka sai kutunku
Sunan ka bai ɓacewa
Har tashin duniya
Jukan Musa ɗan Maliki
Gamdaren Amadu
*Turken Waƙa: Jikan Musa ɗanmaliki Gamda-aren Amadu*[36]

### 3.8 Sarkin Katsinan Gusau,

Jagora: Sadaukin Maza rinjayayye,
Mai Gusau shirinka daban da suwa
'Yan'amshi: (Kamar zube na Jagora)
Jagora: Gagari na Yari
'Yan'amshi: Gagari gaba na Yari
Kai ka karya maza
Sadaukin Maza rinjayayye
Mai Gusau shirinka ka daban da suwa
Jagora: Jikan Sambo yau ka fashe hushi
'Yan'amshi: ƙasar Gusau duk kai ad da ita
Sadaukin Maza rinjayayye
Mai Gusau shirinka daban da suwa
Jagora: In ana rabon gado ga gida
Su yan gida su ad da shiya
ɗan gardama to banda kaya
Sadaukin maza rinjayayye
Mai Gusau shirinka daban da suwa
*Turken Waƙa: Sadaukin Maza Rinjayayye, Mai Gusau Shirinka daba da suwa*[37]

---

[36] . Waƙar Dagacin Gabake, Alhaji Mu'azu [anmalikin Gabaken {auran Namoda. Na halarci taron da wannan mawaƙin ya gabatar da wannan waƙar a ranar 23/9/1983 a garin Birnin Magaji

[37]. Ɗanƙwairo ya yi ma Sarkin Katsinan Gusau Waƙa, Alhaji Kabir [anbaba OFR, na samu wannan waƙa a shafin sada zumunta na "Dandalin Masoya Ɗanƙwairo" a watan fabrairu, 2021" .

### 3.9 Sarkin ƙayan Maradun,

Jagora: Na Macciɗo gamda 'aren Sarkin Rwahi ƙisake,
'Yan'amshi: Rai ya daɗe kKamdaren Baraya
ɗan AMadu tsayayye
Ko dauri ba ya wargi
Jagora: Gagari gaba
'Yan'amshi: Mai jiran faɗa da arna
ɗan Amadu tsayayye
Ko dauri ba ya wargi
Jagora: Ya zo da lafiya Mamman
'Yan'amshi: Sauka lafiya da girma
Jagora: Ya je da lafiya Mamman
'Yan'amshi: Sauka lafiya da girma
Jagora: Ya je da lafiya mamman
'Yan'amshi: Sauka lafiya da girma
ɗan Amadu tsayayye
Ko dauri ba ya wargi
Jagora: Wani ɗan Sarki mai ciki da ƙushi
'Yan'amshi: Ko can ba arziki ga rai ba
Banga alamar riƙo ga rai ba
Jagora/'Yan'amshi: Ku san ba a sarauta da tsinbiran
ɗan Amadu tsayayye
Ko dauri ba ya wargi
Jagora/'Yan'amshi: ɗan Sarkin Musulmi
Na S/Bauran Dange mai wuyak karo
Bindiga ne mai jiran at tayai
Ba jimirin twakala ga rai ba
Muhammadu ba Jirimin twakala ga rai
Mai gaskiya yahi mai ƙarya
Mai hankali yahi mai hauka
An san maɗacci da ɗwaci
An san namiji zuma akwai hwaɗa
Amman Amadu tsayayye
Ko dauri ba ya wargi
*Turken Waƙa ɗan Amadu tsayayye ko ɗauri baya wargi*[38]

---

[38] . Waƙar Sarƙin {ayan Maradun, Alhaji Muhammadu Tambari. Sardaunan Maradun Alhaji Bashari Atiku ne ya samar da wannan Waƙa a cikin kaset na Rikoda a watan Yuni 1986, a garin Maradun Jihar Zamfara.

### 3.10 Sarkin |urmin Bakura

Waƙar Sarkin Ɓurmin Bakura, Alhaji Yusuf III.

Jagora : Na yi mahwalki
'Yan'amshi : Dokin da yas saye ya bani
Jagora : Sarkin Ɓurmi jan damo
'Yan'amshi : Maidaga Uban Zagi
Jagora : Mai Ɗankadu da Rini
'Yan'amshi : Guru baka takuwa
Kowat take ka nan
da nan ya hwaɗi
Mai Bakura na Yari
Bida arna jiƙan na Abu
ɗan Ibrahim.
*Turken-Waƙa Mai Bakura na Yari, Ba a kai ma reni,*
*Bida arna jikan na Abu ɗan Ibrahim*[39].

### 3.11 Sarkin Fulanin Bunguɗu,

**Jagora:** Sarkin Fulanin Bunguɗu,
**'Yan'amshi:** ɗan'Amadu ka hwashe haushi,

**Jagora:** Da hurar wani gwamma kunu na.
**'Yamamshi:** Ga wani nan ya yi ɓatatta,
Ya saki kaza ya riƙe Kolo,
Na zaka in maka murnam
Allah ya yi ka Sarki,
Sarkin Fulanin Bunguɗu,
ɗan Amadu ka hwashe haushi,
*Turken Waƙa: Na zaka in yi maka murna, Allah ya yi maka Sarki*[40]

### 3.12 Waƙar Banagan Maru,

Jagora : Ibrahimu na Barga
'Yan'amshi : Jikan Abdu na Alƙali
mai bargad doki
Bai ɗau wargi ba
Kak ka yadda da reni
na Malam ɗan Mamman
Jagora : 'Yan Sarki ku bi Sarki

[39] . Waƙar Sarkin |urmin Bakura Alhaji Yusuf na III. Na samu wannan waƙar a wajen abokina Labbo Kundum a ranar 27/8/ 2021

[40] . Alhaji Lawal Garba Ɗanƙwairo Maradun ne ya rera mini wannan waƙa da bakinsa a ranar 27/8/2021

’Yan’amshi : Su tashi kai akushi
Kowaƙ ƙi biyayya ya hwaɗi
Bai ɗau wargi ba
Kak ka yadda da reni
na Malam ɗan Mamman.

*Turken Waƙa : Bai ɗau wargi ba, Kak ka yadda da reni na Malam ɗan Mamman*[41].

### 3.13 Waƙar ɗan-Alin Birnin-Magaji

Jagora: Ya bida maza
Alh. ɗan Ali na Ummaru
‘Yan’amshi: (Kamar a na Jagora)
Jagora: Na Alkali Dodo
‘Yan’amshi: Maƙi gudu na Alkali Dodo kake
Ya shira kayan faɗa
ɗan Ali ya shira kayan faɗa
Ya bida maza
Alhaji ɗan Ali na Ummaru
Jagora: Wandara ɗan Wandara
Jagora/’Yan’amshi:Na Alh. ɗanmaliki
Jagora: Tsoron ka a kai
‘Yan’amshi: Ba a da damar faɗa maka
Jagora: Arna shakkak ka saukai
‘Yan’amshi: Ba su da damar faɗa maka
Ya bida maza
Alhaj. ɗan Ali na Umaru
Jagora: ɗan Korau jikan Korau
Ka ab bajini gida
‘Yan’amshi: Kuma kai ab bajini dawa
Ya bida maza
Alhaji ɗan Ali na Ummaru
Jagora: ɗan Alin B/Magaji Mode
‘Yan’amshi: Mulki nai yai yawa
Mulki nai yai yawa
Jagora: Mutanen ƙaura sun faɗi
Haz Zurmi da Mariki
Sunash sheda mani
‘Yan’amshi: Mulkin ka da nasara
Jagora: In dai kaje gabas
Ka miƙe har Maliya
‘Yan’amshi: Sun san mulki kakai

[41]. Tattaunawar da na yi da Alhaji Lauwali Garba [anƙairo kamar a ɗure na 38

Jagora: In kuma kayi Yamma
Har Ikko cikin Legas
'Yan'amshi: Sunsan mulki kakai
Jagora: In kuma ka yi Arewa
Har Dosso cikin Nijar
'Yan'amshi: Sun san milki ya kai
Jagora: In kuma kai gusun
Kaje kamaru da Gamdare
'Yan'amshi: Sun san Mulki ya kai

Jagora: Ya na da darajja Najeriya
'Yan'amshi: ɗan Ali yana da mutunci a Najeriya
Shi ba ƙarami bane
Ya bida Maza
Alhaji ƙan Ali Na Ummaru
Jagora: Sarkin Taurin Birnin Magaji
'Yan'amshi: ɗan yalla yabo ni kai
Jagora: Ba Najeriya ga kaɗai ba
Dan nan har ƙasar waje
In dai Maganat Yauri ce
Jagora'Yan'amshi: Ko ƙumba tasan Tauri ka
Turken Waƙa: Yabida Maza. Alh. ɗan Na Ummaru[42]

## 3.14 Sarkin Mafaran Gummi

Jagora : Toron Giwa Muh'd ɗ/Mamman
'Yan'amshi :Toron Giwa Muh'd ɗ/Mamman
Jagora : Kashe gwangwanin maza
Muhammadu ɗ/Mamman
'Yan'amshi : Toron Giwa Muh'd ɗ/Mamman
Dattijo mai halin a yaba mai
Sarkin Mahwara
Garnaƙaƙin maza
Wanda baya da tsoro
Jagora : Kwarkon ruwa kware
'Yan'amshi : An shedi sarautag gidan ga
Bata wuce ka
Sarkin Mahwara
Garnaƙaƙin maza
Wanda baya da tsoro
Jagora : Sarauta ga mai rabo take
'Yan'amshi : Na ga marar rabo

[42] . Waƙar Sarkin Birnin-Magaji, [an Ali Alhaji Muhammadu Mode Usman. Hajiya Goshi [an-Ali Mode Usman ce ta tallafa mini da wannan waƙar a cikin kaset na Rikoda a ranar 19 ga Fabrairu, 1985

Ya yamutce rai nai
Sarkin Mahwara
Garnaƙaƙin maza
Wanda baya da tsoro
Jagora : Mugun Madambaci Mamman
'Yan'amshi : Buga ga hanci
Buga ga idanu
Sarkin Mahwara
Garnaƙaƙin maza
Wanda baya da tsoro.
Musa Ɗanƙwairo Maradun
Waƙar Fada /S/Mafaran Gummi,
Muhammadu Maidabo.
Turken Waƙa :
*Turken Waƙar :Sarkin Mahwara, Garnaƙaƙin maza wanda baya da tsoro*[43].

### 3.15 Sarkin Yaƙin Kware ta Shinkafi

Jagora: Gogorau Bahago,
'Yan amshi: ƙi garaje,
Muhammadu Sarkin Yaƙi,
Sarkin Kware Allah yana riƙa ma,

Jagora: Mai sulken yaƙi,
'Yan amshi: Sarkin Yaƙi Namijin duniya ne,

Jagora: Na zaka in gai sai,
'Yan amshi: ƙwairo Uban kiɗi,
Don ya yi daidai,

Jagora: Uban Sani, Uban mainasara,
'Yan amshi: Hannu Ba ka tsoro,
Muhammadu Sarkin Yaƙi
*Turken Waƙa: Sarkin Kware Allah yana riƙa ma*[44].

[43] . Alhaji Aminu Mai Kaset Talatar Mafara ya taimaka mini da wannan waƙar a cikin faifan Sidi, a ranar 3/3/2002

[44] . Waƙar Sarkin Yaƙin Kwaren Shinkafi wadda aka samo a hannun Malam Musulimu Ladan Maru a ranar 27/8/2021

3: 16 **Sarkin |urmin Moriki**

**Jagora:** Muhammadu ɗan Mamman,
**‘Yan Amshi:** Mai Moriki ana saunar halinai
Muhammadu ɗan’Alu
Gagarau Namijin Daagaa tsayayye
*Turken Waƙa*: *Muhammadu ɗan’alu gagarau namijin daaga tsayayye*[45]

Naɗewa

Daga cikin masarautun ƙasar Zamfara masu daraja ta ɗaya guda shaɗaya (11) da masu daraja ta biyu shida (6) ake da su a yanzu, Ɗanƙwairo ya waƙe masrautu kusan goma sha-shida. Ga samfurinsu nan a sama an lalabo. Wasu waƙoƙin sai ahannun abokai masu sha’awa da tanadin waƙoƙin baka, wasu kuma a hannun ‘yan uwan sarakan da aka yi wa waƙen aka nema suka bayar. Fahimtar wannan maƙala shi ne, idan da ba don wannan dama da ta taso ta tunawa da Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun ba, da fasihancinsa, da wasu waƙoƙin sun ɓace ɓat idan ba a lalabo su an adana su a cikin irin wannan siga ba.

Makaɗa Musa Ɗanƙwairo ya taka gagarumar rawa wajen adana tarihin zamunna, musamman na saraki a kundin waƙoƙinsa, wand aba don ire-irensa ba, da tarihin masarautu da al’ummun Hausawa (Zamfarawa) ya afka cikin ruwayoyi kamar yadda shi kansa tarihin sheakarn Makaɗa Ɗanƙwairo ya zama cikin ruwayoyi mabambanta.

[45] . Waƙar Ɗanƙwairo ta Sarkin |urmin Moriki Muhammadu Aliyu. Na samu wannan waƙar a hannun Lauwali Garba Ɗanƙwairo a ranar 27/8/2021

**Kammalawa**

A cikin shafin gabatarwa an kawo silalen yanar gizo wanda aka adana wannan maƙala a cikinsa. An yi haka ne domin tanadin tarihin Makaɗa Musa Ɗanƙwairo ya shiga taskar adani ta zamani. Haka nan ake tsamanin idan masoya tarihin Hausawa da waƙoƙinsu suka ci gaba da kulawa za su riƙa bitar wannan tarihi da ƙara yi masa sharhi bisa ga wanda muka yi a yanzu, har jikokimmu masu zuwa bayammu su samu. Idan hakan ta samu, to buƙatar wannan maƙala ta biya.

Tsayawa ga kundayen da Shaihin malamin Hausa Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau ya tara domin fahimtar wane ne Musa Ɗanƙwairo, ya rage mini wahalhalun yin bitar ayyukan da suka gabaci wannan maƙala domin shi Farfesa Gusau ya san Musa Ɗanƙwairo sanin da duk wani manazarci bai yi masa ba. Na samu damar cewar hakan, domin tun Farfesa Gusau bai san irin rana mai kamar ta yau za ta zo ba, ya shiga gonar nazarin waƙoƙin baka da yanaye-yanayensu na ƙasar Hausa gabaɗaya, inda su Musa Ɗanƙwairon suke tinƙaho da ita, domin cikinta aka haifi kakaninsu da iyayensu da su kansu har suka kwanta dama, suka bar 'ya'ya da jikoki a ciki kamar yadda muka gani a yanzu. Aikin Alhaji Sani kan wasu salailai a cikin wasu waƙoƙin Musa Ɗanƙwairo ma, ya samu albarkar ayyukan Farfesa Sa'idu Gusau duk da cewa yana da nasaba ta jini da Musa Ɗanƙwairo ta gefen mahaifiyarsa (shi jikan Ɗanƙwairo ne).

Fatar wannan maƙala shi ne, manazarta su himmatu wajen nemowa da taskacewa da rattabewa da adana tarihinsa da waƙoƙinsa da hotunansa, da hotunan waɗanda ya yi waƙa domin nazarin rayuwar Alhaji Musa Ɗanƙwairo da ta iyalansa ta naɗe tarihe-tarihe da yanaye-yanaye na ƙasar Hausa kacokam. Dalilin cewa haka shi ne, ko ni ƙaramin almajiri na samu ilimi mai tarin yawa a cikin wannan nazari da na yi, kaɗan daga ciki akwai: tarihin yaƙe-yaƙen da suka wanzu a tsakanin sarakuna a ƙasar Hausa. Da tarihin daulolin da sika wanzu a Afirka, da tarihin gidajen Sarakunan mulki na ƙasar Zamfara da na Daular Usmaniyya. Haka nan na fahimci tattalin arzikin Hausawa da ƙasar Hausa a da har zuwa yanzu yana nan tsakanin noma da kiwo da fatauci da kasuwanci duk a dalilin waƙoƙin Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun. Na koyi darussan zaman duniya, da ladubban zama da mutane daga ƙumshiyar waƙoƙin Musa Ɗanƙwairo kamar haƙuri da zama mai ƙwazo da kuma tanadi.

*A nan zan taƙaita da cewa lallai su Musa Ɗanƙwairo sun yi babbaƙu, sun yi wasulla, sun yi ta yi, har sun sabka, don haka sun ilmantu in dai hwa waƙata, sai dai a sara musu ba a kushe su, duk hwa mun yarda.*

**Manazarta**


Ado, A. (2019) *Ra'o'in Bincike Kan Al'adun Hausawa*, Government Printing Press, Katsina.

Birnin Magaji, I.M (2018) "Duniyar Makaɗan Fada Jiya da Yau." A Cikin Taguwa Multi- Disciplinary Journal of Humanities Katsina: Umaru Musa 'Yar'aduwa University, Katsina, Katsina State.

Birnin-Magaji, I. M. (2020) "ƙasar Zamfara a Bakin Makaɗan Baka, 1900-2000", Maƙalar da Aka Gabatar a Taron ƙara wa Juna Ilmi kan Daular Zamfara, Wanda Tsangayar Fasaha ta Jami'ar Usumanu ɗanfodiyo ta Shirya a ranakun 27-29 ga Fabrairu.

Birnin Magaji, I. M (2020) "Makaɗa Ibrahim Narambaɗa A Fadojin Ƙasar Hausa" Takardar da aka gabatar a taron Ƙasa da Ƙasa Kan Makaɗa Ibrahim Narambaɗa Tubali, A Jami'ar Bayero Kano Ranar 15-17 ga Watan Satumba ,2019

Birnin Magaji, I. M. (2020) "Sauye-Sauye na Ci Gaba ga Manyan Masarautun Jihar Zamfara1900-2000 (The Transformation of Emirates in Zamfara State) (1900-2000)" Maƙalar da Aka Shirya Domin Bugawa a Mujallar da ake Shiryawa Shekera-Shekara a Tsangayar Fasaha da Ilmin Addinin Musulunci ta Jami'ar Usumanu ɗanfodiyo, Sakkwato.

CNHN (2006), *ƙamusun Hausa* na Jami'ar Bayero Kano, Ahmadu Bello University Press, Zariya.

Chafe, K. (2016) "Jihar Zamfara: Tarihinta da ƙalubalenta da Ribatarta a Tarayyar Nijeriya" Maƙalarda aka Gabatar a Taron da Gwamnatin Zamfara ta Shirya na Cikar Jihar Zamfara Shekarau Ashirin da Kafawa wanda aka Gudanar a watan Oktoba 2016, a Gusau, Jihar Zamfara.

ɗanjuma, M.S. (1982) "Gudummuwar Waƙoƙi ga Rayuwar Bahaushe" Takardar da ya Gabatar a Sashen Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero

Gusau, S. (1984) "Nazarin Zaɓaɓɓun Waƙoƙin Baka na Hausa" Cyclostyled Edition, Kano Department of Nigerian Languages, Bayero University.

Gusau, S.M. (1988) Waƙoƙin Makaɗan Fada: Sigoginsu da Yanaye-yanayensu. Kundin Digiri na Uku: Kano Jami'ar Bayero, shafi na 170-177

Gusau, S. (1996) *Makaɗa da Mawaƙan Hausa*, Bench Mark Publishers, Kano

Gusau, S. (2014) *Waƙar Baka Bahaushiya*, Bayero University, Kano Inaugural Lecture no 14.

Gusau, S. M. (2019) *Diwanin Waƙoƙin Baka Juzu'i na Huɗu* Wasu Waƙoƙin Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun (1909-1991), Century Research and Publishers, Kano

*Infaƙul Maisuri* : Taƙaitaccen Tarihin ƙasashen Tukururu na Sarkin Musulmi Muhammadu Bello, Fassarar Sidi Sayuɗi da Jean Boad, (1974)

Longman, (2003) *Active Study Dictionary*, Edinburg Gate.

Sani, A. R. (2019) "Nazarin Salo a Cikin Wasu Waƙoƙin Musa Ɗanƙwairo Maradun", Kundin Digiri na Biyu, Usmanu ɗanfodiyo, Sakkwato

Tambuwal, I. (2002) "The Facinating Emirates of Zamfara State, Matani kan Tarihin Masarautun Zamfara" da ke Jiran ɗab'i. A Publication of Zamfara State Council of Chiefs

Rataye na I: Tattaunawa da Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun

TATTAUNAWA DA MAKAƊA MUSA ƊANKWAIRO MARADUN WADDA AKA YI A RANAR 8-11- 1974.

MAI GABATARWA

LAWAL ISAH

Yau Wannan Fili namu inda kukan ji munyi hira da Makaɗa da Mawaƙa, gani Allah yabani Makaɗa Ɗankwairo. Yau hirar nan tamu zaku jini tareda Makaɗa Ɗankwairo a cikin Filinmu na tarihin Makaɗa da Mawaƙa.
Toh! Tunda dai nafaɗi Makaɗa Ɗankwairo, kowa ya sani!,
Tafashe dai ne!
Hahhhh, Turaye, to abinne da taushi da Kotso kusan duk tafiyarsu ɗaya. To shi yasa kusan na ɗan yi suɓul da baka, nace tafashe, To kotso na Makaɗa Ɗankwairo ke kaɗawa.

LAWAL ISAH: Makaɗa Ɗankwairo in ka yarda in tambayeka?

ƊANKWAIRO: To na yarda

LAWAL ISAH: Kai asalinka mutumen ina ne ?

ƊANKWAIRO; Niyya?

LAWAL ISAH; Awo

ƊANKWAIRO; ASALINA MUTUMEN BAKURA NE

LAWAL ISAH; Ina take? Kasar Barno ko Adamawa?

DANKWAIRO; A'A ƘASAR SAKKWATO

LAWAL ISAH; Bakura wannan ta Ƙasar Sakkwato?

DANKWAIRO; Eh

LAWAL ISAH; To Madallah, to yanzu Makaɗa, shin cikakken sunan kenan Ɗankwairo koko a kwai wani?

ƊANKWAIRO; Lai Lai akwaishi

LAWAL ISAH; Ya ? Minene? Don nima ban saniba kuma kusan Jama'a da yawa ma basu saniba.

ƊANKWAIRO; Ni Musa nake

LAWAL ISAH; Ina aka samo labarin Ɗankwairo?

ƊANKWAIRO; Ina aka samo labarin Ɗankwairo?, tsohona yayyi bara har yarrasu, niko ina ƙarami ina da shekara bakwai sai nafara amshi sai aka jiya, sai aka samin sunan maigida.

LAWAL ISAH; Allah ya jiƙan Rai, to yanzu tun yaushe kafara wannan sana'a ?

ƊANKWAIRO; Ni ?

LAWAL ISAH; Eh, ta kiɗi

ƊANKWAIRO; Tun inada shekara bakwai aka fara sani ina amshi

LAWAL ISAH; Kana ɗan amshi?

ƊANKWAIRO; Eh, ina ɗan amshi, to tsoho na yayyi kiɗa sai ya miƙani ga Wa na, Kurna.

LAWAL ISAH; Kurna Wan ka ne ?

ƊANKWAIRO; Eh, Wa na ne, uban mu guda dashi.

LAWAL ISAH; Na'am! Saboda haka Kai wannan sana'a ta kuɗi gado ne.

ƊANKWAIRO; Awo, gado ce.

LAWAL ISAH; Watau ba hayenta kayyi ba?

ƊANKWAIRO; A'a, watau Kaka na wanda aka ce ma Makaɗa Kaka, shi akkaka na wanda yahaifi Ubana.
LAWAL ISAH; Shi kuma Baban ka yattashi ya kama wagga sana'a.

ƊANKWAIRO; Shiko Tsoho na Usman yake Ɗankwanaga Shiko ya kama wagga sana'ar

LAWAL ISAH; Duk anan aka yi ku a Bakura?

ƊANKWAIRO; Eh

LAWAL ISAH; Umnmm to yanzu a wannan lokaci chan kana da shekara bakwai da ka fara wannan amshi, shima maigidan abubuwan yake kaɗa wa?

ƊANKWAIRO; Ehhh, iskesu nayi garai tunga Kaka na.

LAWAL ISAH; Yanzu wajen shekara nawa kenan?

ƊANKWAIRO; Wajen shekara nawa kenan? . . In gani . .

LAWAL ISAH; Kai shekarar ka nawa?

ƊANKWAIRO; Ni ? Sittin

LAWAL ISAH; Ka fara wannan kana ɗan shekara bakwai, kaga hamsin da uku kenan

ƊANKWAIRO; Yawwa!

LAWAL ISAH; To yanzu Makaɗa, koda yake waɗannan Samari naka kasan basukai sittuna au sabau'na da akance, kai da ka Kai wajen sittin, su wajen 'yan arba'in ne nan Kusa kusa, saboda haka basu wuto wannan lokaci ba amma kana iya ɗan takulo mani irin waɗannan waƙoƙi chan nada sadda kake ɗan amshi ?

Ko da Kai ɗai ne, yaran in ba za su iya ba, kaɗan taɓa min waɗanchan waƙoƙin da kake ɗan amshi, wace irin waƙa ce aka fara da ita ?

ƊANKWAIRO; Wadda aka fara da ita inji tsoho na?

LAWAL ISAH; Eh ta Tsoho

ƊANKWAIRO; Ta Tsoho! Hahahaha wadda kan nissani to waƙar Sarkin Kaya Iro, saboda ina da shekara 5 anka taso dani daga Bakura, anka dawo dani Maradun, watau komin tsoho na ya fara wanda naji da kunne na watau Maradun.

LAWAL ISAH; wace ka fara ji wadda kake iya tunawa ?

ƊANKWAIRO; wadda na fara ji ?

" Gagarau namijin duniya Iro'

"Ɗanna Gwaggo kana lafiya Iro"

"Gagarau namijin duniya Iro', Ɗanna Gwaggo kana lafiya Iro"

"in za ka Sakkwato babbar hanya tun dar Gora har bisa Rini har bisa Damɓo har Ɗan Kaiwa har 'yar Tsakkuwa har Nasarawa har zuwa . . . .

*Gagarau namijin Duniya Iro"

LAWAL ISAH; hahahaha to naga de Makaɗa, to watau sai dasu ake kiɗa

ƊANKWAIRO; Sannan ba'a haife su ba.

LAWAL ISAH; Ayya, yau da gobe har an haife su

ƊANKWAIRO; Lokacin da aka yi ta ni ina da shekara Tara.

LAWAL ISAH; bayan ka fara cin gashin kanka, wace waƙa ka fara ta kanka, a yi muna ita tare da ƴan amshi. Waƙar da ka fara yi taka ta kanka ba kana amsawa wani ba.

ƊANKWAIRO; Waƙar da na fara yi ta kaina ta Ƴandoto na yi ma.

LAWAL ISAH; To yaran na iya amsa ta ko?

ƊANKWAIRO; Eh

LAWAL ISAH; To a waƙa ta

Wakar YANDOTO

Jagora/Amshi; "bida Arna bai yadda akamai wargi ba, mai wuyar gaba yahana karya  Ƴandoto'. ×2

JAGORA; Ƴan Sabon Gari na Jekada . . . .

AMSHI; "bida Arna bai yadda akaibmai wargi ba, mai wuyar gaba ya hana ƙarya Ƴandoto"

JAGORA; "Ya hau da lafiya, sauka lafiya uban Sarkin goma ci Marafa Dodo wandara gwarzon Sani"

AMSHI; "bida Arna bai yadda akai mai wargi ba, mai wuyar gaba ya hana ƙarya Ƴandoto'.

JAGORA; "Amadu Sarkin kiɗi na Jekada Mai ta duniya Kurna na Sarkin Ƙaya Ɗankwairo Makaɗin Yandoto.

AMSHI; "bida Arna bai yadda akai mai wargi ba'

JAGORA; "hawan da kayyi randa kazzo Bilbis rannan ka gwada rinjaya Ali Ɗan Muhammadu ka jibge daji da Doki, fadawa gami da zarwa rannan sai hattara sukai, masu gangumma duka suna faɗin bajinin Garewa ya darzazo ɗibgau na Amadu bajinin Shehu, tarnaƙi hana jeka uban galadima, Ali gagarau na ci da ƙarfi ba fasawa uban 'Yandoto, ba fasawa tsayayyen Sarki.

AMSHI; "bida Arna bai yadda akai mai wargi ba, mai wuyar gaba ya hana ƙarya Yandoto"

JAGORA; "Wani ya barkace yana shawagi, aljihu ɗauke da kashin Ɓauna

AMSHI; "bida Arna'

AMSHI/JAGORA; 'wani ya barkace yana shawagin Kade aljihu ɗauke da kashin Ɓauna'

AMSHI; "bida Arna bai yadda akai mai wargi ba'

JAGORA; " inko yayi gardama Dan Sarki na bisa kaiwa, in ko yayi gardama Ɗansarki na bisa kaiwa Kullum.

JAGORA/AMSHI; "ko chan samu gidan sarauta ba fa fushi kasa a daɗe yace masu sai Kun dawo.

AMSHI; "bida Arna bai yadda akai mai wargi ba, mai wuyar gaba ya hana ƙarya Yandoto"

JAGORA; "ko chan samu gidan sarauta ba fa fushi kasa a dade yace masu sai Kun dawo.

AMSHI; "bida Arna bai yadda akai mai wargi ba, mai wuyar gaba ya hana ƙarya Yandoto'.

LAWAL ISAH; hayya!

Chasss (kalangu)

LAWAL ISAH; kar a fasa shi, Sarkin Kiɗa hahahaha
Ɗankwairo a cikin waƙoƙin ka da yawa akwai inda kake cewa zakin kiɗa, Daudun kiɗa Marafan Kiɗa, shin mi kake nufi da waɗannan saurautu ?

ƊANKWAIRO; Watau ƙarin waƙa sukai

LAWAL ISAH; Shi Zakin kiɗa, mi ke aiki nai ?

DANKWAIRO; Ƙari

LAWAL ISAH; Shike Kari

ƊANKWAIRO, awo Kuma duk ƙari sukai, watau su biyu kenan su azzakin kiɗa, wanga ko shi a daudun kiɗa

LAWAL ISAH; To amma Ɗankwairo, na sani da yawa na kuma ji, koda yake bai riko ban gani ba lokacin da kake tareda yayan ka, shi Kurna, kana yi mishi amshi, bayan shi maigida ya rasu kenan koh!

ƊANKWAIRO; Eh

LAWAL ISAH; sa annan kana yi mashi amshi, sannan sai kabi wanka Kurna, to inason wata waƙa wadda take ta Kurna ce ba taka ba, a ɗan raira mana ita

ƊANKWAIRO; To, to, to madalla.

LAWAL ISAH; Tunda shi babu shi yakwanta dama, ya rigamu gidan gaskiya, aɗan tuno munadashi in ɗan ji wata waƙa irin tashi

ƊANKWAIRO; To, to

WAKAR KURNA DAGA BAKIN ƊANKWAIRO

JAGORA; ' kurum mai ban tsoro kware ba zagawa, mai hana noma Sarkin Kaya Zaki Ɗan Iro'

JAGORA/AMSHI;

kurrum mai ban tsoro, kware ba zagawa, mai hana noma Sarkin Kaya Ɗan Iro'

JAGORA; "ga Kurna yana Kidi munzo inda Zakin Kiɗi yacce ba gudu ba'

JAGORA/AMSHI;
' ga Kurna yana kiɗi munzo inda Zakin kiɗi yacce ba gudu ba'

JAGORA; Mai jama uban Yandoto mai ban tsoro

JAGORA/AMSHI; Mai ƙarfin arziki ba'a ja mai, wani ja da kai ka buge mai baki, wada yashsha wuya yassaki tun rannan waddara ko washsha wuya ban

kurum mai ban tsoro kware ba zagawa, mai hana noma Sarkin Kaya Zaki Ɗan Iro'

JAGORA; Mai sarautar kwana ya wuce mai sarani Gandu ya hi mai tabe ai ko chan da ɗai ba guda ne ba

AMSHI; kurum mai ban tsoro kware ba zagawa, mai hana noma Sarkin Kaya Zaki Ɗan Iro

JAGORA/AMSHI; Na Ummaru kai adda halin mutanen dauri

AMSHI; kurum mai ban tsoro kware ba zagawa, mai hana noma Sarkin Kaya Zaki Ɗan Iro

JAGORA/AMSHI; Kowa na biyan kiɗi, kai dai wane sai aji labarin ka

JAGORA; " Sallah gata ta masu sai an bani Kubta da wandon zane inko anƙi bani kuɗɗi in daƙale kiɗa. . . .

LAWAL ISAH; hahaha Toni kada a daƙale mani kiɗin nawa

ƊANKWAIRO / LAWAL ISAH; hahahahaha

LAWAL ISAH; Kamin inci gaba, wai shi kotso dami a ke yin shi?

ƊANKWAIRO; icce wanda a ka yi nai?

LAWAL ISAH; Awo

ƊANKWAIRO; ana yi nai da ƙirya

LAWAL ISAH; Iccen Kirya ?

ƊANKWAIRO; awo

LAWAL ISAH; To ita fatar fa? Akwai wata iri daban

ƊANKWAIRO; ta Akuya dai ta

LAWAL ISAH; Ko wace iri?

ƊANKWAIRO; A' a ba kowace iri ba! Watau wadda ay yarinya hakanga

LAWAL ISAH; Kamar Burguma

ƊANKWAIRO; Mai Burguma, mai Kamar wata bakwai haka ko shidda ko biyar

LAWAL ISAH; Na'am, to wannan daudawa daudawa da ake liƙawa hwa?

ƊANKWAIRO; Shiko nake na. Watau shiko wada yake. ƙasa, Jar ƙasa aka biɗa kamar ta ƙunƙuwa

LAWAL ISAH, Kamar ta Suri

ƊANKWAIRO; Yawwa! to ita aka ginowa inji masu yi, to sai su gama da ɗiyan aduwa, ƙwayar ɗiyan aduwa, to nan sukavyi sai suyi nake. Mukam bamusan yadda sukayi nai ba amma munsan kayan aikin

LAWAL ISAH; Mai kaɗa shi ba shi ka sassaƙashi ba ?

ƊANKWAIRO; A'a bashi ka sassaƙashi ba

LAWAL ISAH; Saye kukai?

ƊANKWAIRO; Awo, saye mukai

LAWAL ISAH; Na'am

ƊANKWAIRO; Haka yake muna saye nai Sule biyu

LAWAL ISAH; shi Ɗan dunƙulen?

ƊANKWAIRO; Awo, shi Ɗan Dunƙulen. Amma ba musan yadda suka dafa shi ba amma munsan kayan aikin. Da ƙasa ta ƙunƙuwa da ƙwayar ɗiyan Aduwa

LAWAL ISAH; Mahaɗar dai baku sani ba, wannan nasu ne kuko ku bugashi yayi zaƙi

ƊANKWAIRO; muko bamuda ikon yi sai dashi

LAWAL ISAH; To Makaɗa baya ga kiɗan sarauta, ai ina zato kana da wani kidi?

ƊANKWAIRO; Eh, na ɗan taɓa kiɗin Noma

LAWAL ISAH; Kiɗin Noma ? To dami ake kaɗa wa? Ganguna ne koko?

ƊANKWAIRO; Awo, da ganguna nayi

LAWAL ISAH; Yanzu wannan baya iya bin kotso ?

ƊANKWAIRO; yana bi

LAWAL ISAH; a ɗan taɓo mana irin kiɗan noman nan inji

ƊANKWAIRO; Toh madalla

LAWAL ISAH; A faro

ƊANKWAIRO; To Madallah

JAGORA; "Ya rigasu gona mai Kalmen wuce maza Ɗan Musa, Ya rigasu gona

JAGORA/AMSHI; "A gaida magajin Abdu . . . .

Mai Galmar mutan gabas, wata huda yakai yana Kuiye manya manya huce ba'a sashi Mara Mara

JAGORA; " ka zama tambari uban Gangumma na ɗan kurciya bajinin bari mai fashe baicin ƙasar giye ka zama gagaren maza dan tukku

AMSHI; "ka rigasu Gona mai Kalmen wuce Maza Dan Musa

JAGORA; Ya kai Kulla an ƙera mashi diga guda am maisheta kacciya ga fashin diga kwano ga ɓotar sule guda an gyareshi an hawas, Goje baya kakare wasu bangallai yaka tayarwa mai karfi kamar habar bisa ya ɗora turmuzar kuiye . . . . Kuiye ca ka Kai Katangar Sarki

AMSHI; "Ya rigasu gona mai Kalmen wuce maza Ɗan Musa

JAGORA; "A gaida magajin Abdu, jadarma na sale gwarzon Sani' ai tunda kayyi nohi, wanzamenga bai zamo raggo ba. Mata da maza suna faɗin Mamman ka iya aski, bajinin sale gwarzon Sani masu danin hannu

AMSHI; "Ya rigasu gona mai Kalmen wuce maza Ɗan Musa

JAGORA; Ɗan Musa da yayyi mana gyara naji daɗi, mai askar da ta sha kaifi

AMSHI; "Ya rigasu gona mai Kalmen wuce Maza . .

JAGORA; "Wanzamen da yayyi mani gyara saiga gwatsine ina ta cizon baki Ƙwairo ina hakuri da jijji mai kiɗi sai nacce abinga yazan ƙeta

JAGORA/AMSHI; "Ya rigasu gona mai Kalmen wuce Maza Ɗan, Ya rigasu gona

JAGORA; Aski Ɗan shawa ne

AMSHI/JAGORA; To missa ido ruwa har yassa ana gani beke na.

AMSHI; " Ya rigasu gona mai Kalmen wuce maza Ɗan Musa

JAGORA; A gaida Ɗan Sule Ɗan Dammu na Bello jikan Yakubu, mulmulalle kake ba lamtsa ba, cata baya jan Kara don noma

AMSHI; " Ya rigasu gona mai Kalmen wuce maza

JAGORA; "Ɗanmusa ya ƙulla kwando bakwai na gyaɗa ya kamma galma yana dahi yana rufi, mai shukakga bammu ga ya cimma ba

AMSHI; "Ya rigasu gona mai Kalmen wuce maza Ɗan Musa

JAGORA; "A gaida magajin Abdu shatima na sale gwarzon Sani

AMSHI; "Ya rigasu gona .

LAWAL ISAH; hahahaha, na tsaida kai ne nima in gaisheka, dan saboda wannan gatanan ka saketa amma har yanzu ana jin ta

LAWAL ISAH; Tun shekara nawa aka yi ta wagga

ƊANKWAIRO; Waƙarnan tayi shekara goma sha takwas

LAWAL ISAH " To yaushe kenan rabonka da yin wannan waƙa ta noma?

ƊANKWAIRO: Yanzu?

LAWAL ISAH: Um

ƊANKWAIRO : Kuma yanzu abinda a shekarata rabo na waƙar noma sam

LAWAL ISAH: Um

ƊANKWAIRO: Yau komai a shekarar Yandoto da sarauta

LAWAL ISAH: Wannan na Tsahe?

ƊANKWAIRO: Um

LAWAL ISAH: Watau an dai jima, an samu biyar ko Shida

ƊANKWAIRO: Eh Shekara Shida ne kuma maraba ta da kiɗan noma sam

LAWAL ISAH: Amma gata har yanzu ba a manta ba

ƊANKWAIRO: Awo

LAWAL ISAH: Hahaha Sai aka koma kiɗan sarauta

ƊANKWAIRO: Awo

LAWAL ISAH: To makaɗa an taɓa zuwa wasu wurare an taɓo wasu wurare an gano wasu wurare ban da ƙasar Sakkwato kawai? Akwai wasu wurare da aka zagaya wanda kiɗi kawai ya kai ka?

ƊANKWAIRO:  I to na dai zo Daura,

LAWAL ISAH: Na'am

ƊANKWAIRO: Na zo Katsina

LAWAL ISAH: Na'am

ƊANKWAIRO: Nazo Katsina na zo Daura

LAWAL ISAH: Daga nan dai sai can ƙasar Sakkwato?

ƊANKWAIRO: Awo

LAWAL ISAH: Yanzu, in na tambaye ka?

ƊANKWAIRO: Haka

LAWAL ISAH: Akwai wata rana cikin waɗanda shekarun nan naka hamsin har da ƴaƴa?

ƊANKWAIRO: Akwai wata rana da aka yi wani abun armashi, wani abun daɗi wanda har yasa ba zaka iya mantawa da wannan rana ba? Don lallai mutum Ɗan adam tum ba mai sana'a ba ma,

ƊANKWAIRO: Eh

LAWAL ISAH: A sami wata rana lallai yasan a samu wani abu, wannan rana kam har in koma kabari na kam .

ƊANKWAIRO: Eh to akwai ta

LAWAL ISAH: To wacce ce?

ƊANKWAIRO: Wato ranar da ban mancewa game da wagga sana'a tawa.

LAWAL: Na'am

ƊANKWAIRO: To nayi wani kuɗa

LAWAL ISAH: Um

ƊANKWAIRO: Yankuzo

LAWAL ISAH: Na'am

ƊANKWAIRO: To nidai bakin iyakar kiɗi na har komawa ga masu gari

LAWAL ISAH: Um

ƊANKWAIRO: Sai ƙaruwa nake kullum ba raguwa ba

LAWAL ISAH: Na'am! Tana ɗaya daga cikin ranakunka kenan na sa'a

ƊANKWAIRO: Eh

LAWAL ISAH: Tun daga rannan dai abun sai daga karuwa kake samu

ƊANKWAIRO: To lallai ban taɓa kiɗi iri nai ba

LAWAL ISAH: Ko rannan ne aka yi wata waƙa, sai ni Ɗanƙwairo mai toho? Daga nan abun ya tohu? Hahahahaha

ƊANKWAIRO: Hahahaha

LAWAL ISAH: Tun da har ka tuna da wannan rana kuma tana ɗaya daga cikin abinda kake alfahari da su, mi aka riƙa cewa a wannan wurin? Wane waƙe aka riƙa yi?

ƊANKWAIRO/YAN AMSHI: "Tafe yake da noma

"Zuciya tai tana gona Mamman

"Tsaye yake ga noma

ƊANKWAIRO: "Kogon Yankuzo akwai ƙwazo

YAN AMSHI: Daudun kiɗi mu gai sai ×2

"Zuciya tai tana gona Mamman

ƊANKWAIRO: "Uban gidan Kakale

YAN AMSHI: Uban gidan Garba Ɗan dagaji

"Ɗan asali ba a tamushe nai ×2

ƊANKWAIRO: Masu gari da a ƙasas Tsahe

YAN AMSHI: Sun san noma yana da lada

ƊANKWAIRO: Masu gari da ƙasar Tsafe

YAN AMSHI: Sun san noma yana da daɗi

Hankali nai yana gona Malam,

Tahe yake da noma

ƊANKWAIRO: "Mai ikon da baya noma

Kuɗɗin gari a kai mai

Kuɗin jangali a kai mai

Albarkar ƙasa a bashi

Ɗan Sarkin da kagga bai riƙa aiki ba

YAN AMSHI: Ya bada iko nai

Tun da ya bada hannu

Zucciyatai tana gona Mamman

Tahe yake da noma × 2

ƊANKWAIRO:  "Kai dud dai abinda kag gada

Shi kake ganin gaba nai ×

ƊANKWAIRO: Ɗan Mama nayi ma shawara

Wàƙag ga wadda niyyi

In dai tayi kyau faɗa mani

In ko ta karkace faɗa min ×2

waƙa abin sayarwa ce

Mu sayar mai ya bamu kuɗɗi

Ya bamu doki

Gami da kaya

YAN AMSHI: Zucciyatai tana gona Mamman

Tahe yake da noma

LAWAL ISAH: Hahaha.  Makaɗa ikon Allah!
Kace in ta karkace ya gaya ma?
To kai dai bata karkacen ba. Hahahahaha duk da yake an rabu da ita, sai naji bata karkacen ba tana nan dai tahe

ƊANKWAIRO: Wai abokina ne makaɗi na bawa labari. Nacce in ta karkace ya hwaɗamin, inko ta karkace hwaɗamin. Nace waƙa abin sayarwa ce ya bani kuɗɗi ya bani doki gami da kaya. Yako bai

LAWAL ISAH: Na'am

ƊANKWAIRO: In Allah yaso

LAWAL ISAH: Makaɗi wata tambaya da zan sake yi maka

ƊANKWAIRO: Haka

LAWAL ISAH: Watau na sani duk wato Ɗan'adam yana da wani abu na jiki nai wanda ya fi so, koda ƴaƴa gareka koda kuwa sun kai ɗari Allah zai jabarta maka son ɗaya fiye da sauran.

ƊANKWAIRO: Haka hwa

LAWAL ISAH: Saboda haka cikin waƙoƙin ka ko akwai wata wadda ba don mai ita na baka kuɗi ba,  ba don mutane suna cewa tana da daɗi ba, a'a kai gare ka dai kana jin daɗin ta a zuciyarka. Akwai irin wannan waƙa?

ƊANKWAIRO: In Allah ya yarda

LAWAL ISAH: " To wacce ce a rera mana ita?

ƊANKWAIRO : To Madallah

Ya ci garin maza Ɗan Shehu.......

LAWAL ISAH: " Nima na yaba muku ƙwarai da gaske. Zakin kiɗi, Daudun kiɗi da kai da Marafa. Lallai na yaba muku, lallai akwai ƙwazo. Sai inji makaɗanma wani wuri kafin ya taso kun yi gaba, har wani kuma da kuka ce ku huɗu ma menene menene? Ya mutum ɗaya ke daku? A wace waƙa ce shin wai? Inda kace ku huɗu duk azanci gareku.

ƊANKWAIRO: Ta Yandoto ta

LAWAL ISAH: To tuna min da waƙa inji

ƊANKWAIRO/ YAN AMSHI: Shirya kayan faɗa mai gida Tsahe

Ali Ɗan Iro ba ka ɗauki raini ba

YAN AMSHI: Shirya kayan faɗa mai gida Tsahe

Ali Ɗan Iro baka ɗauki raini ba ×2

ƊANKWAIRO: " Mai lihiddan faɗa

Ginshiƙin Shamaki

Baba shirgin ƙaya

Mai wuyar ratse ×

ƊANKWAIRO: Na Magaji Ƴandoto jikan Maman

Ɗan Alasan na Turaki mai gayya

ƳAN AMSHI: Shirya kayan faɗa mai gida Tsahe

Ali Ɗan Iro baka ɗauki raini ba

Toron giwa kake mai garewa Ali

Ba a faɗa ka tilas a kauce ma

Inda ka zaka zamanin yaƙi

Da maza ba su ɗaukar rigimarka

Ko mazaizai na farko na asalitan,

Tun azal Ali ab ba a jure ma

Shirya kayan faɗa mai gida Tsahe

ƊANKWAIRO: Kyawon Ɗan Sarki talatin

Ɗan Sarki in yayyi sittin

Bai gaji gidansu ba ta bace mai

Sai biɗar jalli

Ai dubun jakkai

A samu na shan dawo ka da alalace

Shirya kayan faɗa mai gida Tsahe

ƊANKWAIRO: Duk makaɗan da a Tsahe nai jam'i

Har baƙin har ƴan gidan su duka

Babu mai kulla mai ƙulla waƙa kamar tawa ×2

Ga makaɗi ya shirya waƙa tai

Sai a amsa mashi ba a ƙara mai

In na ƙulla waƙa a ƙara min

Mu huɗu duk azanci garemu

Shin ƙaƙa mutum guda za ya rabke mu?

Shirya kayan faɗa mai gida Tsahe

Ali Ɗan Iro baka ɗauki raini ba

ƊANKWAIRO: Batun kiɗi ko baku nan yi mukai

Mun yi ƙidan baƙi mun yi wasulla

Munyi tarihi yanzu ilmi mukai tun da mun sauka

In hwa waƙa ce, duk mun san yadda za mu ƙulla ta

In ance mutum mai mutum mai tujara ne

Sai ya haifi ɗa mai turajar nan

In an ce mutum wane samna ne

Sai ya haifi samna haƙiƙan ne

In Allah yauwa mutum ƙwazo
05/09, 4:48 amɗ Honorable Ibrahim B/Magaji: Alhaji Lawal Isah: Hahahahah, hehehehe. To lalle kai kam Makaɗa an koyad dakai kuma ka ɗauka. Lalle an koyad dakai kuma ba a yadda gida ba ƙwarai dagaske.

Ɗanƙwairo : To Madalla.
Alhaji Lawal Isah: Dama dai muma mun rutso lokacin tsohwahhi muji yadda suka yi nasu abun.

Ɗanƙwairo : Haka nan hwa.

Alhaji Lawal Isah : To shin yanzu Makaɗa shin su waɗan nan irin Waƙoƙi naka shin su kan hwaɗo ne haka nan, koko kukan zanna a gida ayi bitaw waƙa a shirya ta tukun ta shiga ka sa'anan a hidda ta ga sarari?
Ɗanƙwairo : I, to waton in mun ka tashi yin ta kam wadda muka so ta zama abun tcishi to sai mun yi ta dag ga gida, in mun ka yi ta dag ga gida ko in daji mun kayi ta kuma mun ka koma gida in bamu manta ba to sannan mu koma muyi ta gida muna ta jawo wani abu muna sawa....
Alhaji Lawal Isah : Kullum tana ƙaruwa...
Ɗanƙwairo :Kullum tana ƙaruwa tana yaɗo
Alhaji Lawal Isah : Ummh
Ɗanƙwairo :To kaji wada taka girma.
Alhaji Lawal Isah : To yakan ɗauke ku tsawon lokaci, yanzu kamar misali sai nik kawo wani abu kamar in ce ga rediyo nan...
Ɗanƙwairo : Ummh
Alhaji Lawal Isah: Sai in kawo rediyo in aje in ce Makaɗa Ɗanƙwairo ita nike so ai ma waƙa, ya ɗauke ku kwana nawa, ko mako nawa, ko wata nawa kahin ai mata doguwar waƙa kamar ta minti goma?
Ɗanƙwairo : Haka..
Alhaji Lawal Isah: Kwana nawa ana gida ana shirya wa a kawo wannan ƙashin baƙi a cire, a kawo wannan a cire...
Ɗanƙwairo : Ummmh..
Alhaji Lawal Isah : Ayi kamar wata nawa?
Ɗanƙwairo :Waƙa guda?
Alhaji Lawal Isah: I, waƙa guda.
Ɗanƙwairo : At!
Alhaji Lawal Isah: Iyye, hehehehe, a'a ba ƙure ka zani yi ba yanzu ince gata ayi.
Ɗanƙwairo : A'a ai naji, naji misali wanda kayyi
Alhaji Lawal Isah: Ummmh
Ɗanƙwairo : Kamar waƙa guda?
Alhaji Lawal Isah: Na'am!
Ɗanƙwairo : To in an kace muyi ta...
Alhaji Lawal Isah:Ummh
Ɗanƙwairo : Wato mai kaiwa minti goma kacce?
Alhaji Lawal Isah: I, mai kaiwa kamam minti goma.
Ɗanƙwairo : To ko mai kaiwa minti ashirin..
Alhaji Lawal Isah: Na'am!
Ɗanƙwairo : To in mai mun ka koma gida wato in mun ka shirye ta to zamu yin ta...
Alhaji Lawal Isah: Ummmh
Ɗanƙwairo :To mun ka samu kamam mu ukku ɗinga...
Alhaji Lawal Isah:Na'am!
Ɗanƙwairo : Ka jiya, to mun kayi ta, to mun ka yi ta mun ka buga abun Kiɗi mun kayi ta da waƙad da kiɗin, to shi kenan mun ka aje Kiɗin ga, mun ka duƙam mata to ai ga na biyu ga Kiɗin ga guda in mun ka koma na biyu shi kenan munti ashirin muna yi nai.
Alhaji Lawal Isah:Ba ku tashi ba?
Ɗanƙwairo : Ummmh, munti ashirin tsakanina da yaran ga wato ba minti goma ba har ashirin muna kai, awo

Alhaji Lawal Isah: Hehehe
Ɗanƙwairo :To in ko mun ka samu mai haske
Alhaji Lawal Isah :Ummmh
Ɗanƙwairo : To wato mun ka hwara ta, mun ka hwara ta to lalle in ya zamanto tayi haske ham munti talatin muna yi...
Alhaji Lawal Isah: Nan da nan... Ummmh
Ɗanƙwairo : Ga waƙa guda?
Alhaji Lawal Isah: Ummmh
Ɗanƙwairo : Saboda wanga in yayyi wanga jawabi, wanga wani jawabi shi kai. Daɗa in mun ka taram mata wato ance ma wato wane hwa kokowa garai ko dambe to lalle kashe ka shi kai..
Alhaji Lawal Isah: Awo
Ɗanƙwairo :To lalle ka shirya, in kana shiryawa ka shirya.
Alhaji Lawal Isah: Na'am!
Ɗanƙwairo : To lalle in Kak kashe shi ka ci gaba
Alhaji Lawal Isah: Duniya ta jika
Ɗanƙwairo : To duniya ta jika, to ba ka san daɗa ƙoƙari ka kai ba?
Alhaji Lawal Isah:Ƙwarai dagaske.
Ɗanƙwairo : Haka waka take
Alhaji Lawal Isah: Sai a hana ido bacci
Ɗanƙwairo : To wato an kace ga irin abin da aka so kayi, a kaso aga misalin ta an kace to muna son waka mai minti goma, ko waka mai mai minti ashirin, ko waka mai minti talatin, to wato duk iyaka mutum shi ce ya emmuna bakwai guda to in mun ka hwatsa Kiɗin sai hwa mun hwara Kiɗin, to in mun ka hwara da Kiɗin mun kaji tayi, wata mukan yi ta in ba Kiɗin in mun ka yi sai muji bata yi ba.
Alhaji Lawal Isah: In ba Kiɗin?
Ɗanƙwairo : Awo
Alhaji Lawal Isah: To yanzu Makaɗa tun da dai kai wannan sana'a saka ka aka yi ciki ba kai kasa kan ka ba, tun da ɗan shekara bakwai yanda ka fara koyo baka san daɗin ta ba, ba kasan wuyat taba, ba kasan amfanin ta ba. Yanzu da ta zama itace sana'ar ka taɓa da na sani?
Ɗanƙwairo : A'a
Alhaji Lawal Isah: Kace kai dai wannan sana'a dai da na sani tun hwarko dai waɗan da suka jawo ni ciki sun cuce ni?
Ɗanƙwairo : A'a
Alhaji Lawal Isah: Ni kam randa Allah yassa an ka koya man wanga abu tun ina amshi..
Alhaji Lawal Isah: Ummh
Ɗanƙwairo : Ana sammani, to randa nih hwara na kaina Kiɗin noma...
Alhaji Lawal Isah : Ummmh
Ɗanƙwairo : To ni hah waɗan da, hah tswahhi na ni ka jinƙan su. Ni hayyau banyi da na sani ba game da ita.
Alhaji Lawal Isah: Ita ce komi?
Ɗanƙwairo : Awo ita ce komi
Alhaji Lawal Isah: To Allah shi yi taimako
Ɗanƙwairo :In yunwa tak kam mini niƊ ɗauki abin Kiɗi na bani jin ta
Alhaji Lawal Isah: Yanzu ta na yayewa?
Ɗanƙwairo/Y/Amshi /Alhaji Lawal Isah: Awo.. Hehehehe

Ɗanƙwairo : Tun ga Kiɗin noman kuma ga Kiɗin ikon hac cewa nikai ga Kiɗin ikon bani komi
Alhaji Lawal Isah: Na'am!
Ɗanƙwairo :Diba abin da ak kama Kiɗin iko na sosai da sosai..
Alhaji Lawal Isah:Ummh
Ɗanƙwairo : Shekara shidda, to ba ka san daɗa ni han na zure ba?
Alhaji Lawal Isah: Awo ƙwarai dagaske. To yanzu wai kai yadda aka yaye ka kai a cikin wannan sana'a ka taɓa yaye naka yaro ya tashi ya kama gaban kai nai?
Ɗanƙwairo : Ga sunan
Alhaji Lawal Isah : Yanzu su kan ci gaban kan su waɗan nan?
Ɗanƙwairo : I, ƙwarai
Alhaji Lawal Isah :Tahi ba ka
Ɗanƙwairo : Bani nan..
Alhaji Lawal Isah: Sai su yadda Tsoho su yi gaban kan su?
Ɗanƙwairo : Kiɗin noma kam ban ce ma Kiɗin iko ba
Alhaji Lawal Isah: Eh, eh
Ɗanƙwairo : Kiɗin noma
Alhaji Lawal Isah: Sai su tafi baka?
Ɗanƙwairo :Bani nan
Alhaji Lawal Isah: To ara muna guda yanzu ya ɗan sara muna wani irin nasa
Ɗanƙwairo : To Ɗangaladima taɓa mai
Ɗangaladima :
Garba ya gyare gona
Y/Amshi :
Mazan ƙwarai na
Ambaya jikan
Kwasau
Ɗangaladima :
Kai kasada
ɗan mai kasada×2
Y/Amshi :
Na Miko ci toha
ɗan mai gayya
Ɗangaladima :
Kare bai zuwa
gidan Kura
Ko ya zo ka na ishe
ya zwaga
Baya sallama ciki
Y/ Amshi :
In kau ya shiga ciki
Kana ishe ya zan
rummace
Babu hwashi
Ba hwasawa
Kana ishe kashi

walwatce
Garba ya gyare
gona
Mazan ƙwarai na
Ambaya jikan
Kwasau
Ɗangaladima :
Yanzu mu ka kiɗi
Y/Amshi :
Manya sai
karmanci
Ana rawa
Ana loga
A tsaya kuma
ana bugan
wani ƙaton
wando
Garba ya gyare
gona
Mazan ƙwarai
na Ambaya
jikan Kwasau
Ɗanƙwairo :
Duw wanda kag
ma hanya..
Alhaji Lawal Isah: Ahaaha
Ɗanƙwairo /Y/Amshi :
Shi ka hwara illakka
Kaza bata yin miya
in ga Zabo.
Alhaji Lawal Isah: Tsoho yai ma yara karambani, yai ma yara shishshigi
Ɗanƙwairo : Eheeehee
Alhaji Lawal Isah: Yaji abun baya iya yin shiru, wato baka iya yin shiru?
Ɗanƙwairo : Wato jawabi sun kayi man, ja na sun kayi
Alhaji Lawal Isah: Ya sun kace?
Ɗanƙwairo : Wai cewa sun kayi dauri ni ka Kiɗin aiki, sai sun kace man yanzu wai sai karmanci.
Alhaji Lawal Isah: To sai kace masu yaya?
Ɗanƙwairo : Ni ko nicce duw wanda kag gwada ma hanya shi ka hwara rena ka, Kaza ba ta yin miya in dai ga zabo.
Alhaji Lawal Isah/Ɗanƙwairo /Y/Amshi : Hahahahah
Alhaji Lawal Isah : Wato sun yi kaɗan sai dai in ka hwaɗi?
Ɗanƙwairo : Madalla.
Alhaji Lawal Isah/Ɗanƙwairo /Y/Amshi : Hahahaaa.
Alhaji Lawal Isah: Wato ashe ku kan yi haka yaku-yaku?
Ɗanƙwairo : I

Alhaji Lawal Isah:  Kaga yara! Ga Tsoho zanne.. hahahahah. To Ɗanƙwairo lokaci na ko lokacin da muke dashi na hira da kai ya na tahiya, ya yi nisa. Amma yanzu ita wannan sana'a me kake ganin ta, sha'anin kaɗe-kaɗen nan da waƙe-waƙen nan shin nan gaba kau zata ɗore, ko ko zata riƙa mutuwa ne?
Ɗanƙwairo :Ni kam daɗa ban san nuhi ba.
Alhaji Lawal Isah: Wai ga dai yanzu abin da zamani na kawowa, ina aka tasammawa?
Ɗanƙwairo : Ni dai yanzu abin da nig gani yanzu kam ba aw wad dauri ba.
Alhaji Lawal Isah: Abubuwan dai suna sukurkucewa?
Ɗanƙwairo : Awo.
Alhaji Lawal Isah: Saboda haka ma kana jin nan ma gaba kaɗan in a kace bayan baku aka ce ba Waƙa irin waɗan nan abubuwan ba za kayi mamaki ba?
Ɗanƙwairo : I, bani mamaki.
Alhaji Lawal Isah: Abin ya na ta ƙara...
Ɗanƙwairo : Tun da na ga alama.
Alhaji Lawal Isah: To yanzu kahin in yi bankwana da kai ina son in yi zaɓi son ka, akwai wata Waƙa da nike so, sa'anan kai kuma in baka dama ka yi naka zaɓin, ka yi taka waƙai.
Ɗanƙwairo : Haka
ɗ05/09, 7:04 amɗ Honorable Ibrahim B/Magaji: Alhaji Lawal Isah: Wata Waƙa na nan da kake cewa ga wando tugage, ko ya na kashin mangwaro ko mi ne ne?
Ɗanƙwairo : To
Alhaji Lawal Isah: A'a wani wanda ake cewa ummh, mi ne ne ya na ta Kiɗin tambari ya na tallam magani?
Ɗanƙwairo : To wo
Alhaji Lawal Isah: Ban san kowa ce Waƙa ba ce, amma hahahaa, to ai mani ita zaɓi son ka ne wannan, nike son ta, ai mani in jiya.
Ɗanƙwairo :To
Alhaji Lawal Isah: Ummh
Ɗanƙwairo : To
Y/Amshi :

Irin gidan Sama'ila
Alƙalin Sakkwato
Ba a jan ka zamani
Mai jama ya tuɗai

Ɗanƙwairo :

Dodo na Ɗangaladima

Y/Amshi :

Na Sa'idu rai ya daɗe
Baban Sarkin Zagi
Irin gidan Sama'ila

Ɗanƙwairo :

Kwairo na taho jiyara

Y/Amshi :

Mai turu Ƙanen
Makaɗa Kurna
Shiryayye nit taho

Ɗanƙwairo :

Ƙwairo na taho jiyara
Mai turu ƙanen
Makaɗa Kurna
Y/Amshi :
Shiryayye nit taho
Bani zullumin Waƙa
Ɗumi ya na zube
garemu
Ga wasu yan kurkutu
Ɗanƙwairo :
Alƙali Abubakar
Y/Amshi :
Ba mamaki na gohe
Wandara kai aka tsoro
Shi yak kashe
tsageranci
Ba ayi mai shisshigi
Irin gidan Sama'ila
Alƙalin Sakkwato
Ba a jan ka zamani
Ɗangaladima :
Mai kyautad da babu
tambaba
Ɗanƙwairo : Haka hwa
Y/Amshi :
Kana babu karmanci
Kowa nag gane ta
Ya san rinjayayye
yay yi ma
Irin gidan Sama'ila
Ɗanƙwairo :
Dokin da yab bani
Y/Amshi :
Kowa nag gane shi
yasan gun mai ƙarhi
yah hitto
Ɗanƙwairo :
Kuma rigad da yab
bani
Y/Amshi :
Kowa nag gane ta
Ya san gun mai
girma tah hito
Irin gidan Sama'ila
Alƙalin Sakkwato
Ɗangaladima :

Mai kyautab biyan
bufata
Y/Amshi :
Alƙalin Alƙalai
Sai godiya ni kai
Ƙwairo duw wada
aka kyautas so
Alƙali ya yi man
Alhaji zamanin ka
nagode
Ɗanƙwairo :
I
Y/Amshi :
Tun da ban talauci
Suturaƙ ƙwarai
Da ingarma
Ga kuɗɗi swahe
dut
Irin gidan
Sama'ila
Alƙalin Sakkwato
Ɗangaladima :
Daudu an yi ma
doki
Marahwa shi da
swace
Mu ko a bamu
kubtoci hadda
wanduna
Da dai an biya
Y/Amshi :
Don mi ba kai
kaɗai ka bauta ba
In da kayyi waƙa
Kiɗi mu kai
Muna ƙari
Mui ta yi ma...
Irin gidan Sama'ila
Alƙalin Sakkwato
Ɗanƙwairo :
I, kuna yi
Alhaji Lawal Isah/Ɗanƙwairo /Y/Amshi :
Ba a jan ka zamani
Alhaji Lawal Isah: Ba a jan ka me? Ku ruhe..
Y/Amshi :
Irin gidan Sama'ila

Alƙalin Sakkwato
Alhaji Lawal Isah: To shi kenan.
Ɗanƙwairo :
Dodo na
Ɗangaladima
Alhaji Lawal Isah: A'a to ai shi kenan. To ai ya yi gaskiya lokacin ya yi nisa. Ina son in ji shawarar da zaka ba wanda kag ga yanzu ya na son ya shiga wannan sana'a taka. Sai wani yaro ga shi haka matashi ya kama wannan sana'a, sai yazo ya ce ya na son shawara mu kuka kamo kuka runguma har Allah ya taimake ku kuka zama haka, sai kace mashi yaya?
Ɗanƙwairo : To sai in ce mai to zamani dai ya sake.
Alhaji Lawal Isah: Ummh
Ɗanƙwairo : To amman dai in zaka yi tunda ka gada gare ni to ɗamri aniya in arzikin ka ya ƙwatamma abin tcishi kayi, in bai ƙwatamma abin tcishi ba in kaga walaƙanci ka bari.
Alhaji Lawal Isah: Ya watsar?
Ɗanƙwairo : Awo.
Alhaji Lawal Isah: To madalla, to ni dai ba watcad da wannan filin zan yi ba, zan dai yi bankwana ne. Amma tun da aka ce Ɗanƙwairo gaskiya irin abin nan ne da aka ce ranar wanka ba a ɓoyon cibi. In dai an ce Ɗanƙwairo lalle Waƙoƙin Marigayi Firimiya suna ɗai daga cikin waɗan da na hiddo ka. Sune waɗan da suka fi fidda kai a duniya.
Ɗanƙwairo : I
Alhaji Lawal Isah: To saboda haka wurin gaskiya gaskiya ne.
Ɗanƙwairo : In Allah ya so.
Alhaji Lawal Isah:Ina so ka ɗau ɗaya daga cikin Waƙoƙi nai Allah ya jiƙan shi, ya jiƙan mu.
Ɗanƙwairo : Haka.
Alhaji Lawal Isah: Ka ruhe muna hilin da ita.
Ɗanƙwairo : To madalla.
Alhaji Lawal Isah: Ka ɗauko kowace iri.
Ɗanƙwairo : To madalla.
Ɗangaladima :
Ya wuce reni ba ayi
mai shi
Y/Amshi :
Amadu jikan Garba
sadauki
Ɗanƙwairo /Y/Amshi :
Gungurum ƙashin
Giwa
Na Alu ba ka
haɗuwa
Kowah haɗe sai ya
tare maƙoshi
Ɗangaladima :
Amadu ya samu duniya
Ya kau gwada ya samu
duniya
Yai alferi

Ya riƙa ƙanne
Ya riƙa yaya
Ya riƙa bayi
Ya riƙa barwa
Ran Jumu'a
da Ƙarfe biyu
Ran nan yaƙi
yac ci Amadu
Niyyi kuka
Niyyi baƙin rai
Nit tuna Allah
Ni masa murna
Da walaƙanci
Y/Amshi :
Gara shahada
ga Musulmi
Don ba illa na ba
Ɗangaladima :
Da walaƙanci
Y/Amshi :
Gara shahada
Ga Musulmi
Ba illa ne ba
Ya wuce reni
ba ayi mai shi
Amadu jikan Garba
sadauki
Ɗangaladima :
Allah nufa kazo yawo
da niya
Y/Amshi :
In ga duniya
Ɗanƙwairo in ƙara
azanci
Mai Kotso in sheƙe
ayata
Ɗangaladima :
In san Kano
In san Zazzau
In san Katsina
In san Daura
Kuma da Kazaure
Y/Amshi :
Don ko da ɗai ban
san su ba ko can
Ya wuce reni ba ayi

mai shi
Ɗangaladima :
Shi Amadu in za ya
unguwa
Ko yau ko gobe
Bai tafiya
Sai ya tafi Sakkwato
Y/Amshi :
Ya iske wa nai
Su tara dangi
Su yi bankwana
Ya zo ga hubbare Malam
Shehu
Ya yi jiyara
Ya samu albarkak kakanai
Da ɗiyan Shehu da jikoki nai
Ya zo gare su
Ya samu albarkar Tswahhinai
Ya tahi Wurno
Ya tara dangi
Su yi bankwana
Ya zo ga Hubbaren
Mamman Bello
Ya yi ziyara
Ya samu albarkar kakanai
Ya tahi Raɓah
Ya tara dangi su yi bankwana
Ya zo ga Hubbaren Ibrahimu
Ya yi ziyara
Ya samu albarkar Tsoho
nai
Ya tahi Gwandu
Ya tara dangi suyi bankwana
Ya zo ga Hubbaren Abdullahi
Ya yi ziyara
Ya samu albarkar Kakanai
Don haka nan
Ba ka da gehe
Amadu kowa na ƙamnakka
Baka Sheri
Baka barin wani
Yayi Sheri
Sai alheri
Amadu sai alheri
ɗai ya ka hwata
Ya wuce reni

ba ayi mai shi
Amadu jikan
Garba sadauki
Ɗangaladima :
Bangon tama
Mai wuyar iza
Bajinin Sir Kashim
Uban Zagi
Bello ɗan Hassan
Ɗanƙwairo :
Haka hwa
Ɗangaladima :
Mai martabar Ɗanhodiyo
Mai Martaba
Mamman Bello
Mai martabar
Abdullahi
Mai martabar
Attahiru
Mai martabar
Moyi da Attoh
Da uwad daje
Mai martabar
Isan Kware
Autan Shehu
Mai martabar
Ibrahimu
Y/Amshi :
Mai ƙahon karo
Sadauki
Ɗan Sadauki
Kakannin ka waliyan Allah ne
Ba a ba'a ba ko can
Ko lahira muna taulahi
Muna nan can wajjan
hannun ka na dama
Ya wuce reni ba ayi mai shi
Ɗangaladima :
Amadu Bello
Jihar Arewa
Ya ɗauki kwazon
Kowa ce sa'a
Ya gewaya
Y/Amshi :
Ya zo Haɗejiya
Ya tara mutane

Yai masu horo
A zan ka sallah
A zan ka azumi
A hidda zakka
A hidda kono
Ai ta zumunci
Ya riƙa hanyam Mujaddadi
To haka Malam Shehu
Yayyi
Ɗangaladima :
Ya zo Gumal
Ɗangaladima /Y/Amshi :
Ya tara mutane
Yai masu horo
A zan ka Sallah
A zan ka zakka
A zan ka kono
Ai ta zumunci
Ya riƙa hanyam Mujaddadi
To haka Malam Shehu yayyi.